Hajiya shabuki tace" toh meyasa kawai ita nanan bazata fada masa tana sonsa ba tunda kince wannan yar matsiyata ceh nasan shima zeso ace k.'warya tabi k'warya ai"

Mum din nana tace "bazaki ganeba k'awaye ne sosai itada tarinyar tasa kuma son yarinyar yake kamar ransa, bazaitaba yadda ba kuma zeyita kallonta matsayin maciyiyar amana"

Hjy shabuki tace "yoh ai shikenan, badai zamuje gun mlm ba? Da kanshi ze kawo kansa ina gaya miki ita kuma se ta rena kanta"

Mum din nana tace "shiyasa nake son ki k'awata. In har aiki yacika namiki alk'awarin hajji kujera biyu".  Hjy shabuki tace "ai aikin kam kima sawa ranki is complete sbd na yadda da malamin nan sosai"

*••••••••••••✍ by Sajnaa*
*08140813180*
❣👄
[6/1, 12:08 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA KAWAR TAFI*
*GUBA*

🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••••✍ by Sajnaa*

*41↗45*

Sunan allah kawai jahawahir take ambato har ta samu sassauci aranta, shawarar da yaya sahib yabata kenan bayan ta labarta masa abunda ya faru.

Tace "yaya sahib yanzu inaga zan kira nabila awaya in fad'a mata nasan mommah zata taimakemu tanada kirki".

"A'a jawahir base kin kirasu ba, tunda har kikaga mus'ab yamiki hk dere must be sum tin, kawai kibari allah zaisama mana mafita".

"Toh yaya what of mami? Tun safe take asume fah?" Yace "ni inaga mu karb'a adress d'in asibitin can mutafi kawai, mu nemi su taimaka mana suyi mata aikin daga baya ko gidanmu ne se mu sayar mu biyasu kudin". Tace "toh muje Yaya"

_*DR. SHAHID CLINIC*_

Da sauri aka shigar da mami emergency aka sanya mata drip dan yanzu har da k'arin ruwa take buk'ata.

Su jawahir kuma se tambayar likitoci da nurses suke a onah zauga dictor shahid? Sun tambayi mutane yakai biyar amma amsa daya ake basu, cewar yau doctor shahid bayada lokacin duba kowani patient, kuma yayi warning kada kowa yashiga ya dameshi.

Sosai jawahir taji haushinsa, mamin ta na Kwance a sume tun safe sannan yace yau bazai duba kowani mara lfy ba? Afili tace "allah wadarai da mutumin dake biyewa son zuciyarsa akan aikin allah"

Wata nurse ce ta toshewa jawahir baki tajata suka koma gefe kan wani benchi, tace "baiwar allah kirufawa kanki asiri dan allah? Wlhy doctor shahid zai iya yin sanadin kwananki a xell idan yaji wannan mgnr kuma he will send ur mum out of d hospital batareda ya mata aikin ba, doctor shahid yanada zafi sosai mire especially at dis tym dayake cikin matsala"

Jawahir tace "toh meye laifin mu acikin damuwarsa da zaice bazai duba marasa lfy ba". Nurse d'in tace "hmm yau vana tunanin akwae wanda ze iya sauk'o da fushin dr shahid sbd yadda ransa ke bace, dan hk kawai kiyi addu'a kawai allah yasa yasauko amma mgnrki bazai jawo komi ba face wani vacin ran."

Jawahir tace "toh meyene ke damunsa haka?". Nurse d'in tace " _doctor shahid dan uwana neh, ni yar goggonsa ne mahaifinsa kuma kawuna neh, yanzu hk ina zaune ne agidansu doctor shahid, su biyune agun mahaifansu shida addarsa nafisat yanzu hk tana aure a bauchi,

yayi karatunsa ne a us. Dawowarsa daga can befi shekara guda ba yanzu, dad d'insa ya had'a sa aureda wata yar uwarmu zuhra, yanzu wata hud'u kenan da aurensa a lokacin aurensa ne aka bud'e masa sabon asibitun nan da dad d'insa ya gina masa_
_se de abun takaici zuhra batada halin k'warai duk da cewar yar uwarmu ce amma zan bada shedar gskia akanta cewar halinta bana kirki ba ne, tanada bin maza at dsame tym kuma ga shaye shaye, yanzu hk kwanakin baya ya saketa amma dad dinsa yasa aka dawo da ita, again ya dawo da ita ya fahimci tanada juna biyu, jiya yazo da ita asibitin nan ya gwadata, da muka koma gida ya kirani side dinsu yake tabbatar min cikin da ke jikin zuhra ba nasa baneh, wannan ne yasanya ya yanke hukuncin ze saketa kowa ya huta, Amma da ya sanarwa dad d'insa da mum dinsa se sukace basu yadda ba sbd in yayi hkn ze watsar musu da zumunci kuma yanunawa duniya basu isa dashi ba, wai yabari zasu k'ara yimata fad'a zata gyara, kinji damuwar dake damun yaya shahid_

Jawahir tace "toh allah ya yaye masa, ni yanzu yaya zanyi da mami na?"

Nurse din bata bata amsa ba se ga wata nurse da gudu gudunta tana cewa "sister sajida wannan patient da kika sawa ruwa ta farka amma numfashinta sama sama take , kizo dasauri please"

Da gudu suka shiga d'akin da mami take, sosai ta galabaita idanunta sunyi jawur se hawaye takeyi, numfashin kamar ze fita, kuka sosai jawahir takeyi, nurse sajida ne ta lallabeta sukayi waje da ita aka samu akayiwa mami allurar bacci.

••••••••••••••••••••••••••••

Mus'ab da nana sunsha love sosai kafun mus'ab yatafi se da suka gaisa da mum din nana kuma yamusu alk'awarin he will be coming to see her everyday.

Sosai nana sukaji dad'i da mum dinta, a waya aka k'ira hjy shabuki aka sanar da ita cewar aiki yayi kyau mus'ab yazo, shewa tayi tace gani zuwa yanzu.

Ranar bushasha sukayi kamar ba gobe, nana kuwa kamar ba itace marar Ify ba, tawani sakewa yau jin kanta take as d most luckiest lady on d earth.

••••••••••••••••••••••••••••

Mus'ab yana sgiga direct d'akin mommah yashige tana bacci ya sameta dan hk ya dawo falo yanata sak'e sak'e, wani tsanar jawahir ne ke ziyartar zuciyarsa, haushin kansa yakeji dayayi wata alak'ar soyayya ma da ita, nawa jawahir take? Kwata kwata lokaci guda ya mance halin kwarai nata, ya manta soyayyarsa dake tsakaninsu, ya manta yadda yake zuzucewa akanta, da yadda yake burin auranta, ya manta komai se tsantsar tsanar ta dake yawo aransa.

Wayarsa ne tayi k'ara yana dubawa yaga new number ne anyi masa message

_*My sweetberry! Ka isa gida Ify? Allah ya sa hk. Allah ya kara karemin kai*_

_*Ur beautiful darling NANA*_

Kamar ta k'ara haukata sa ya rasa yadda zeyi da ransa,wani k'aunar ta ke k'ara fizgarsa, wayar nabila yakira yace tazo falo ta same sa, da sauri ta fito falon itada sisTer hanifa da wata baby yar addarsu

Tanemi waje tazauna tace "yayanmu angon wani sati ya naganka hk somehow kamar ba lfy ba"? Yace "Lfy amma ba lau ba sister". Tazaro ido tace "me ya faru"?
Ya juyo ya fuskance ta yace _*"i hate jawahir, na tsaneta fiyeda komi just now, kuma na fasa aurenta sbd yanzu nana nakeso nana k.'awar jawahir ita zan aura next week"*_
"Me kake fad'a yaya? Anya lfyrka kuwa?"
"Lfy ta lau nabila, kuma i mean my words, yanzu zan kira dad dina in fad'a masa kuma idan papa yadawo ma muyi mgn daahi da mommah"
Tace "yaya i think bakada lfy, amma banaje nasamu mommah" hanifa kam.mamaki ne ya isheta tace "wlhy ba lfy ba kam,yaya dakaje gidansu nana din me suka baka?"
A fusace yace "i dont know. Wato ma u mean nana tabani mgn ne koh? Toh ki kama kanki akan nana sbd tafimin komai tafimun komai i repeat myself". Dukansu ido suka zaro masa hanifa uwar tsoro tayi gum da bakinta 🤐 tabishi da ido dan tasan ba normal ba! Nabila ne ta dage tace "yaya nana tafi ma komai?". Yace "yess, i mean my words"
Ya fice ya barsu da mamaki.

•••••••••••••••••••••••••••••

Kwana mami tayi tana bacci sbd allurar da akayi mata, jawahir ne ta kwana agun mami itada sister sajida sbd itama a week din tana night duty ne, jawahir kuka tayi tayi sister sajida na lallab'inta takuma umurceta da yin sallah ta rok'awa mamin ta sauk'i ,jawahir taji dadi sosai tare Sallar sukayi addu.'o'i.
Da safe jawahir zata fita nemo abincin sayarwa ta sayo musu, se ga sister sajida a moto, jawahir bata ma lura da wayea moton ba, tana tafiyarta sannu sannu tana kuma kalle kallen kyawun asibitin amma a wayance ba yadda za'ai mata kallon k'auyanci ba..
Sister sajida ne tayi parking moton agaban ta ta leko tana cewa "baby jawahir ina zuwa?" Jawahir tajuyo tamata murmushi tace "sister sajida ina kwana"? Sister sajida ta amsa suka gaisa tace "se ina?" Jawahir tace "zanje sayo abun karyawa ne abakin hanya nan"
Sister sajidaTa jata tace "mutafi cikin office dinmu, d'azu ankawo mun brekfast dina. Ban bude bama yaya shahid ya kirani wai inzo gida in daukoshi he cant drive his car sbd bayajin dadi."
Haka suka wuce office dinsu nurse sajida, wani babban food flask ne shake da abinchi,su koyi ne da chips duk an tarasu in a different bowls. Har dakin da mami take sukaje basu jima da shiga ba ta tashi. da kyar suka lallabeta taci abincin, Jawahir se murna takeyi, sosai tayiwa sajida godiya, sister sajida tace ba komai an zamo daya.

••••••••••••••••••••••••

Mus'ab motsi kadan nana motsi kadan nana abun ya damu mommah sosai yau two days kenan yak'i zuwa gun jawahir Kowa ya kasa gane masa, abun daya ishi mommah se ta bugawa hjyrsa waya.

*••••••••••✍️ by Sajnaa*

*08140813180*
❣👄
[6/1, 12:08 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*•••••••••••••✍ by Sajnaa*

*36↗40*

Se da yamma su mum suka dawo, naba suka saka agaba suka turarata da wani kullin mfn a leda se tari takeyi, se da suka gama sannan hjy shabuki ta kalli mum ymrana dariya tace "daga yanzun hnklnki kwance babu abunda ze hana mus'ab auren nana se dai in ita ta k'i".
Kafun mum tayi mgn nana tace "wai mum hayak'in menene wannan? Ni dai asanina banida cutar aljanu👹 ko mayu👹?"
Mum tace "kar ki damu wannan sinadari ne dazai vaki damar malakar burin zuciyarki mus'ab, nayi hkne svd bazan iya jure ganinki a wahale ba sbd wat banza k'awa" nana tace "amma mum kinf san alak'a ta da jawahir duk da cewar a yanzu nafi jin haushinta fiyeda kowa amma ina gudun bakin duniya kinsan amintar mu ba na wasa bane"
Mum tace "hjy shabuki kin gani koh? Ita kulum amintar su da jawahir takeji ba matsalarta ba, toh in tambayeki, da jawahir da mus'ab wanne kika fi so a cikinsu. In kin zab'i jawahir fine duk abunda zaki fada daga bata kan mus'ab ba ruwana"
Nana tayi rau rau da idanu tace "mum wlhy duk duniya aynzu banida wanda nakejin haushi irin jawahir sbd nasan ita kad'ai ce tamin shamaki da masoyina mus'ab, inajin tsanarta fiyeda sonda nayi mata abaya, na tsaneta fiyeda yadda natsani mutuwa da talauci mum". Mum tace "gud my daughter" hjy shabuki tace "in har kin tsani jawahir kuma kinason mallakar nus'ab dole kibi duk abunda mum dinki zata fada miki kinaji?". Nana ta d'aga mata kai. Hjy shabuki tacigaba da cewa "insha allahu zakiga aiki very soon zakiji muna gud'a agidannan auren d'iya daya tilo, ranar zamusha bidiri"
Nana tace "nagode kuma zanbi duk abunda kukace wlhy koda ze cutardani inhar zansamu mus'ab"

••••••••••••••••••
Jawahir kullum dare tana sallah, shawarar da maminta ta bata kenan kullum tayi sallah tanema ma kanta zaman lfy da mijinta sbd tasaba da wannan addu'am dan kada yabata wahala in anyi auren.
Haka kuwa takeyi, kullum tana rok'awa maminta cikekkiyar lfy, da k'awarta nana, sannan tasa

addu'ar zaman Ify a k'arshe sbd ita acewarta Ifyr maminta da nana shine bikin, in basu samu Ify ba na auren za'ayi ba.
Rayuwa kenan, kana nemawa mutum sauk'i shikuma alokacin yake k'ok'arin cusa maka wutar cuta azuciyarka, allah sarki dole jawahie tace *wata k'awar tafi guba*.

Sosai jawahir tayi kyau ta goge kamar wata yar hjy da alhaji kullum.mamakin kanta take da irin wannan haske datakeyi me kyau ba tareda tayi using Cream s na bleaching masu lalata fatar mace ba.

Mus'ab ma kullum.mgnrsa kenan wai princess dinsa ta fada masa meye sirrin? Tai murmushi tace "mommah ce sirrin ba kowa ba" yace "lalle mommah tayi son kai anan kam, ta ware yarta tabarni" dariya sosai jawahir tayi sannan tace "Ai se ka fada mata in ka koma" haka suka gama lobewarsu yakoma gida.

Zaune suke a falo shi da su nabila , mommah tashigo tadau remote ta canza channel tana cewa "ba jiya kun kalla film dinnan ba neh?" Mus'ab "kai mommah nifa nan kalla ba naje hira kinsani kuma hanifa tafada mun yayi kyau, meye ma sunansa?" Ya juya yana tambayar hanifa, tace *"munubiya"*
Mommah tace " ni nagaki da arewa 24 dinnan sbd banason wannan dan banzan yaron nomis gee,"
Dariya sukayi mus'ab yace "me yin zafafa koh?". Tace "shidai hip hop din nan" nabila suka sa dariya se ga wayarta na ringing da gudu ta haura sama tareda amsa kiran masoyinta.
Hanifa ma tace "ya mus'ab tashi muje kaban Ibrn anty jawa dan ni bazan kali liberty tv ba wollah". Yace "je ki ina zuwa, zamuyi mgn da mommah neh"
Tawuce tana tura baki, ya kalli mommah yace "yauwa mommah kinga jawahir tace batasan wasu events din amma big bross yace tunda yasa hanu ya rubuta ba abunda za'a soke, she must attend dem all, kuma kinsan halinta bazata iya saka wannan rigar tasun ba irin wedding gown dinnan sannan tafito bainal jama'a without hijab ba, meye solution my dear mommah"?
Tai shiru sannan tace "zanyi tunani akai kuma zanyi mgn da big bross din naku, shi yak'i aure shine ze hanaka yin yadda kaso anaka auren"?
Mus'ab yace "yauwa my mommah, dan allah kuyi mgn kinga yau friday sati daya ya saura kawai".
Kamar an mitssine shi ya tashi da sauri, mommah yace "what happen"? A kid'ime yace "mommah nana fa batada Ify wallahy, kuma banje na gaisheta ba, bari naje yanzu". Be jira amsar mommah ba ya fice da key'n moto ahanunsa, mommah dai kanta yakulle batasan waye d'insa bane nana, dan haka takira hanifa take tambayarta, hanifa tace "wai besty'n ba jawahir ce" mommah tace "no wonder, sbd komi na jawahir nada muhimmanci agunsa bare kuma besty'n tah"

•••••••••••••••••••••
Da sauri2 yafito a moton yashige gate din gidansu nana, me gadi ne ya hanasa shiga sbd besan shiba, sukaita jayayya, daga k'arshe yace ace musu mus'ab hussaini kanal ne, me gdin dayaji sunan alhj hussaini kanal da sauri ya bud'e masa yashiga.

Ya aika wata yar aiki dayaga tana yiwa flower bayi, tashiga cikin gidan, nana tana zaune tana kallo daka ganta zakasan ba nitsuwa atareda ita ko kadan, ta kalli yar aikin a hasale tace "uban me kikiazo yi a part din masu gida dan ubanki? Kin debo tsummokara da tsamin jiki zaki kawo mana nan koh?"

Yar aikin tace "sorry madam.wani ne awaje wai mus'ab hussaini kanal yazo dubaki da jiki shine yace inyimasa iso agunki". Da gudu nana ta rungumeta rana cewa "ki rantse , kice wallahy mero"? Mero tace "wallahy dagaske ne yana waje" tace "mero bari nadawo namiki alk'awarin ninka miki albashinki kinji"? Mero tazube k'asa tana godiya nana ta dagota Tasake rungumeta tana tsalle.

Mum dake saukowa daga stairs tace "ke nana? Me zangani? Yar dana haifa acikina ne rungume da yar talaka walakantacciya baiwa"? Nana tace "mum albishir takawo mini mus'ab na waje yaxmzo gunane wollah har naji na warke ma"

Nan danan mum tahau murna. Naba tawuce zata fita mum tace "a'a shigowa zayyi amma kafunnan se na shirya ki na sanya miki turaren da kwalin da mallam yace kiyi amfani dashi inzaku hadu, dan hk muje daki, ke kuma mero kice masa ya iso kuma kice masa nana kinsamu tana wanka neh"

Ya kai five minutes yana zaune afalon ji yayi ya matsu nanan tafito suyi ido hudu, a fili ya furta cewar "i miss u so much nana" a hnkl yaji takun ta, ni dahi duka muka daga idanu muka kalleta, sanye take da wani doguwar riga tasha zanen flowers da stones agaban rigar, kalar blue ce dark roba ce dan hk takama jikin nanan sosai, fuskarta ma anyi mata light makeup, kanta kuma babu d'ankwali se kitson kalaba datayi da k'arin attachment, maha allah tayi kyau sosai, hanunta tray ne na drinks se wani k'amshi takeyi kamar amarya, *(subhanallah mata mu kiyaye, sanya turare gawani ba mijinki ba haramtaccen abune amma bamu d'aukeshi abakin komai ba)*

Ta k:ariso ta zauna se yauk'i take, shikuma yakife ta da eyes kamar yadda nima nayi, amma ni kallon mamaki nake mata shikuma kallon ta yake yana admiring kyawun data k'ara duk da cewar akwai rama sosai tareda ita dazai bayyana maka tayi fama da ciwo.

"Nana ya jikinki"? Ya furta a hnkl, cikin shagwaba tace "ba dai kak'i zuwa dubani ba se yau"? Yace "am sorry nana yanzun ya kikejin jikin nakin?" "Am feeling much better " tafada yayinda hawayen farinciki suka biyo fuskar ta.

Da sauri "noo, nana dont cry mana bakida Ify jada kiyi kuka beside dis ma kinyi kyau in kikayi kuka zaki goge kwalliyar ki" dadi taji sosai tace "ok wipe away d tears for me if u mean ur words" dasauri yace "yes, i meant it nana" yasa hanu yashare mata k'walla, wani shu'umin murmushi ta sakar masa shima murmushin yake mata yace "i miss u so much nana" tace "really?". Yace "yes nd ofcourse, u mean alot to me"

Nikam mamakine ta isheni nace oh ni sajna, shikenan sun asircewa jawahir mijinta, inaji ina gani sukai ta lobewa ba kunya, nana harda kiss tayiwa mus'ab 🙈 ooh allah nah ba yadda zanyi incigaba da zama gidansu nana, sbd i can't take it nima ina taya jawahir kishin mus'ab dinta dan haka gara naje gunta inga meke faruwa.

••••••••••••••••••••••••

"Maami...wayyo mamii nah ya zanyi in kika mutu kika barni mami......mami dan allah kitashi," kuka sosai jawahir takeyi tana rungume da maminta, wata nurse ne ta lallab'a ta suka fita aka shiga duba mami.

Sun dau lokaci sosai kafun afito da mami kan stretcher akayi wani room din da ita . numfashi nafita a hnkl amma bata farfado ba, likita ne ya buk'aci ganin yan uwanta, jawahir da sahib suka shifa doctor din yace jawahir taje waje sbd har ynz bata bar kuka ba, se da tafita sannan yayiwa sahib bayani cewar k'odan mami duka biyu sun samu matsala dole se anyi mata dashen k'oda,sannan jini ta yahau ga ciwon suga.

Hawaye ne ke bin fuskar sahib din , sosai yayi kuka sannan ya tambayi likita solution, likitan yace k'odan wani za'a cire asanya mata, sahib yace likta "kacire nawa kasawa maminmu rayuwarta yafi mana komai"

Doctor yadafa shi "cool down please, be a man ,mace tayi kuka kai kayi wats d difference btw u nd her? ka nitsu kajini inshaa allah ur mum will be ok. Sannan mu bamuda k'wararrun likitoci kan harkar dashen wani abu dan hk akwai asibtin da aka bude dis year amma is private hospital Ba na gomnati baneh. In har kukaje da yaddar allah zata samu lfy, doctor shahid ya k.'ware sosai, yanzu i advise u ku kaita can"

"Ok, doctor kavamu address din , ina dai za'a iya yimata ayau,?". Doctor yace "ba zayyi yuwu ayi mata today ba aikine dayake son nitsuwa da isasshen lokaci, kuma ganin doctor shahid dinma wani aiki ne sbd miskiline sosai, sannan kuma u have to pay first b4 d operation se kun biya kudin aikin wanda ze kai 85 thousand a hasashe na".

Kuka sukeyi dukansu both he nd jawahir .tunanin Su A a ina zasu samu kud'in aikin mami.

Jawahir ne ta daga wayarta ta kira mus'ab tafada masa, tsawa taji mus:ab din yamata sannan yace "ko da wasa kada ki k'ara nema na a kan tsiyatacciyar matar nan dan bani nasa mata cutar ba kuma banida lokacin ki" kuka ta fashe dashi sosae ta durk'usa har k'asa tafara pleading kamar yana ganinta "mus'ab ka taimake Ni duk abunda nai maka kabari in mami na tayi lfy se ka hukuntani"

Ranshi a b.'ace yace"kin ban ajiyan kud'i ne ko meye? Ko uwata ce ba lfy.? Toh in uba nane manajan cbn ma yau banida kudin dazan baki". Nana dake kusa dashi ta karbi wayar dadai lokacin da jawahir "ko sadakina kavani mus'ab zan nemi cikato, lfyr  mami tafimin komai, am in need of ur help mus'ab, yanzune nake buk'atar taimakon ka da gaggawa mus'ab,dan allah kataimake ni......" tafashe da kuka me  ban tausayi.

Muryar nana data jiyo cikin wayar ne yasa ta saurarawa tareda zaro idanu, nana tace" ke yar matsiyata jawahir kike ko waye? Ina gaggawan sanar da ke kifita hanyar mus'ab yafi miki alheri, on ba gaka ba se kinyi dana sanin zuwanki duniya, kiyi kuka da kyau kuma yanzu kika fara, sbd mus'ab nawane yanzu ba naki ba, in ba ki ba ki gane me mgnr ba toh ki saurara da kyau nana Khadija ce yar mum da dad, aminyarki ada" tana fadan hk ta katse wayar.

Jawahir tafashe da kuka tana fadin *"inna lillahi wa inna ilaihir raji'un, allahumma ajirni fi musibati wa akhlifni khairan minhaa"*

Oh poor jawahir,allah ze saka miki😭.

*••••••••••••✍ by Sajnaa*
*08140813180*
❣👄
[6/1, 12:08 AM] Sajna: . 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••••✍by Sajnaa*

*46↗50*

Hjyrsa ta kirasa a waya tayi masa fada sosai akan sabon salon daya fito dashi, amma mus'ab bud'an bakinsa yace " mummy, nasan kina sona, kinason abunda nakeso, kuma bazaki so abunda ze cutar dani ba, kuma a dalilina kikasan jawajir har kikesonta aranki, kina sonta ne sbd ina sonta, mummy ynz banason jawahir kema kidaina sonta please, kiso nana ita nakeso please mum"

Hjyrsa tace "wai wace tsiyace nanan kam kake k'ok'arin maidamu k'ananan mutane akanta, kuma me tafi jawahir din? Ni nasani vazata kai jawahir mutunci da tarbiyya ba sbd masu hali irin na jawahir basuda yawa cikin matan ynz, se an tona, kuma kada ka manta fa an riga anbuga katin nan, sannan ni bazan tunkari dad d'inka da wannan batu ba, u better know, gara kadau shawarar mu kawai , in ka k'i kuma u're d one to deal with him, not me!"

Yace "oh mummy, u too? Kema bakyason abunda nake kenan? Meyasa hk mummy? Mommah tace ba da itah ba, kema kince badake ba, toh dawaye zanyi? Waye zai yimawa su dad mgnr kenan?"

Mummyn mus'ab kam ta gama k'uluwa da wannan d'an iskan batu marar kan gado wai auren nana, kuma abun takaici ma nana din aminiyar jawahir ce, toh ita inta amince akayi bikin nan dawani ido zataga nana da iyayenta?"

Karaf ta katse wayar dan takaici, tasa hanu biyu tana buga tagumi, wayar tane keta ringing amma fir taki dauka sbd tasan mus'ab ne sbd ringing data sa masa daban ne, ko mijinta dad d'in mus'ab bata samasa special ringing ba, sannan kuma ga sunan data sanya masa *luvly one* da manyan baki se yawo yake kan screen d'in.

Missed call takai 12 ita kanta takasa jurewa, ta amsa wayar tace "my son? Ya zanyi ne da baby jawa? I love her so much, ita nakeso as my in law ba nana ba, kaga nasan halin jawahir nana kuma bansan ta ba totally, kayi hkr mus'ab, ni inaji ajikina jawahir is d best wife u will ever have"

Cikin sautin kuka yace "ok mum, tunda bakiso shikenan is okay, nabari"

Hankalinta yatashi sosai tace "a'a my son dont cry please, kasan wani abu?". Yace "no"

tace "ok, i will come to gombe tommorow insha allah, zamu tattauna kaji?".   Yace "ok mummy, se kinzo".  Tace "yauwa fine boy, kada kayi kuka, kaji? Kafa gidan papa akwai k'annenka dayawa dey will laugh at u,".  "Ok mummy se kinzo din, dasafe zakizo ko?".  Tace "insha allah early in d morning zaku ganni".    Sukai sallama dukansu suka aje wayar suka shiga duniyar tunani.

Shi mus'ab tunaninsa mummy'nsa tace batason nana, dole ya hkr kenan? nd again tace jawahir takeso a matsayin surukarta ba nana ba? Shikuma bayason jawahir, nana yake so, ya zayyi kenan? Kuma harga allah mummy'nsa means alot to him, he can't do without her, tanayi masa duk abunda yakeso why not shima just for once yabi zabinta? Kaaaiii, it can't be! Yadda yake jin son nana na fisgarsa bayajin ze iya jure rashinta.

Mummy'nsa kuwa tunaninta shine meye ne yafaru tsakaninsa da jawahir haka? Ita yadda tasani mus'ab d'inta idan aka cireta aka cire daddy'nsa, toh ko y'an uwansa na gidan papa (su nabila kenan) basu kai masa jawahir ba, kuma wacce ta tab'a jawahir ranar ta tab'o jagwal, dan bata mantawa a gabanta ya make autan su nabila wai dan tace tafi jawahir fari.
Da wannan tunanin takira mommah tasanar mata cewar gobe tana zuwa, mommah tace "allah ya kaimu gobe d'in, gara dai kizo yafi, sbd nakasa gane kan yaron nan, bansan meyene nana tayi masa ba"
Mummy ta numfaa tace "wai nikam mommah who d hell is nana? Yar wayece itah? Kuma meye tayiwa mus'ab"?
Mommah tace "aminiyar jawahir ce, yadda ya fadamun wai 'yar gidan alhj ahmad ce ai, yaron daddy'nsa, inaga bazaki rasa sanin alhj ahmad din ba ai"
Mummy tace "what? 'Yar gidan alhj ahmad wanda nasani? Wanda alhj yaje gidansa kwanaki da mukazo gombe?"
"Yes, shi dai, au tare sukaje da mus'ab d'in"
Mummy tace "mommah bazan tab'a yarda mus'ab ya auri 'yar Rahana ba indai ina raye, baza ma afara ba ko da wasa insha allahu".   Mommah tace "akwai matsala ne?" Mummy tace "ba kad'an ba ma kuwa, ke dai mommah se nazo gobe, zan fada maki komai akan Rahana". Mommah tace "toh allah ya kawoki Ify"

••••••••••••••••••••••

_*WASHE GARI*_

Misalin 11 na rana mummy'n mus'Ab zaune tareda mommah, isowarta kenan gidan, suka gaggaisa da kowa tace "hanifa kiramin yayanku mus'ab"
Hanifa tace "to" tawuce tasameshi rike da waya yanata danne danne, tashuga tazauna tace "yayanmu, ina kwana?".  Ya amsa mata  "Ify lau"
"Me kake yine da waya hk ko daga kai bakayi?" Yai murmushi "kun fiye gulma yarannan, mummy na turawa message sbd tacemun zatazo yau early in d morning kuma har yanzu shiru,

yanzy kuma antynku nana nakewa msg"
Tace "toh mummy kam gatacan afalo itada mommah, yanzu ma itatace inzo in kiraka" ta mike tafita.

Dasauri dasauri Yashigo falon yana cewa "u're wellcome dear mumcy" Bata kulashi ba ya nemi guri yazauna, sannan suka gaisa, yace "mummy allah yayi kinzo, ya hanya?".
"Lfy lau,mus'ab inaso ka nitsu ka amsa mini tambayoyin da zanyi maka". Yace "toh mummy insha allah inajinki"
Tace "meye alakar nana da jawahir? Meye alak'ar ka da jawahir? Meye alak'ar ka da nana? Sannan meye dalilanka na yin danyen hukunci wa zuciyarka?"
Ya kalleta ya kalli mommah yace "mummy fa na aza zaki tambayeni ne gidansu nana kuje kuyi mgn amma.......". Be k'arisa ba mommah tace "kinji ko? Abunda yake fama dashi kenan mummy, in dai ba mgnr auren nana akayi masa ba yada wani interest din da zae saurareka"

Mummy tace "mus'ab hk kadawo? Kaida nasanka da halin k'warai, nake alfahari dakai agaban duniya, na godewa allah daya bani da guda daya tamkar dubu, ina alfahari da halayen ka na kwarai, amma mus'ab lokaci daya akan wata mace har momnah ta kasa handling tunaninka? Ita da ta daukeka as her son, ache baku jituwa if she's against nana? me ka zama ne mus'ab? Who the hell is NANA?"
" Am sorry mum, please accept my apology both u nd mommah means alot to me, ba yadda za'ayi na bijire muku kawae dae mummy inason nana ne son da babu wani masoyin dake yiwa wacce yakeso".
Sosai mummy da mommah suka gwalalo idanu suna kallansa😳😳, mummy tace "mus'ab meye hadinka da nana? I mean alak'ar ka da ita?" Tayi mgnr ne cikin sanyin murya. Mus'ab yace "mummy as u know, nana k'awar jawahir ce ko ince aminiya, a dalilin jawahir nasan nana sbd randa nafara ganinsu ma tare nagansu, yanzu kuma bazan kira nana kawar wacce nakeso ba se dai ince itace wacce nakeson"
Mommah tace "mus'ab me kasha neh mun shiga uku? Kada dai yafara shaye shaye ne mummy, do something please in ba hk ba zamu ji kunya" tayi mgnr ne hnklnta atashe.
Mummy ta kwantar da murya tace "Luvly one fadamun mekasha please, let me know, nice mahaifiyarka ka fadamun yaushe kafara shaye shaye?". Hawaye ne suke sulalowa a idan mus'ab , he bend down on his knees, ya rik'e hannun mummy dana mommah yace "Dukanku iyayeba ne, kun sanni kunsan halina, kunsan abunda zan iya da wanda bazan iyaba, uwa uba kunsan tarbiyyar da kukai min.Baku dorani a karkatacciyar hanya ba, dan allah kubar tunanin nafara shaye shaye wlhy banashan komai, sanin kanku ne ko panadol bana sha without prescription of a doctor, kawai ni nasani kun fadi hakane sbd yaddda nake muku mgn with opened mind free, nima kuma bansan dalilin dayasa bana iya boye k'aunar da nakewa nana ba".
Momnah tace "ok stop crying , is okay tashi katafi dakinka, we will talk about d issue kaji?" Kai kawai ya gyada mata yatashi, ta juyo ta fuskanci mummy tace "mummy wayene Rahana? Kumameyene Ibrn da kikace zaki fadamin?
Mummy ta numfasa tace "nasan Rahana wato mahaifiyar nana farin sani tun yarinta"

•••••••••••••••••••••••••••

Yau ne ake shirin yiwa mamin jawahir dashen zuciya sbd doctor shahid yaukam yasaki jiki yana kula da marasa lafiyansa, jawahir se murna sukeyi, sbd sister sajida tace mata za'ayi musu aikin free, jawahir tace "ashe dai tun farko nice ban fahimci halin yayanki ba amma ynzn nagane yanada kirki kaman ke" sister sajida tace "ai yaya shahid zuhra ce kawai ke sanyashi misbehaving, amma in ba hk ba duk family'nmu mata da maza yafi mu sauk'in kai"

Dr shahid ne yafito ya katse musu hirar, idanu ya kurawa jawahir, itakuma gausheshi tayi a mutunce ya amsa sede har yanzu be cire idanunsa akanta ba, sister sajida tace "yaya shahid zaka yi aikin yanzu ne?" Ya juyo with a smiling face yace "yeah, ina bross din nakin?"ya juya yana tambayar jawahir.

Tace "yanzu zaizo yaje sayo katin waya ne" ba'a jima ba yaya sahib yadawo, babu b'ata lokaci aka shiga dashi dan duba kodarsa wacce za'a cire asawa maminsa, sedai anyi rashin sa'a kodarsa itama guda daya ta lalace, daya ce kawai me lfy, jawajir tana kuka tace acire nata asawa mami, yaya sahib yace "kema hkne jawahir tun kina k'arama koda daya gareki me lfy, babu wani me lfyayyan koda acikinmu, hk abbanmu ciwon daya kashe sa kenan in baki manta ba"

Cikin kuka tace "bazan taba mantawa da silar mutuwar abba ba, yanzu ya zamuyi ne yaya sahib , wayyo allah nah😭🙆🏼"

*••••••••••••••✍by Sajnaa*

*08140813180*

[6/1, 12:10 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀

*WATA K'AWAR TAFI*

*GUBA*

🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••• ✍ by Sajnaa*

*51↗55*

Sister sajida ne ta lallab'i jawahir har ta dena kukan nata.

Doctor shahid kuwa has already lost his control, lokaci daya hnkln sa ya tashi ganin yadda jawahir ke rufsa kuka, _*"OH POOR JAWAHIR, MAY GOD HEAL UR MUM"*_Abunda yafada kenan yayinda ya kifa kansa akan teburin sa, yarasa meke masa dadi totally, komai ya dagule

masa, anata kawo masa files na marasa Ify amma ko guda daya yakasa bud'ewa.

Wayarsa ya d'auka ya kira sister sajida, nan danan tashigo office dinsa, ganinsa tayi kansa a kife yanayinsa ya canza, ta ce " yaya shahid me ke damunka? Oh allah na yaya kamanta zuhra mana, nan fa office kake, kula da marasa Ify kakeyi dan allah yaya be a man"

Ya dago idanu ya kalleta yace " have a sit" ta zauna ta fuskance shi yace "hu told u cewar tunanin zuhra nake? Zuhra me takemun da zanyi tunaninta, in banda bak'in ciki me nake samu agunta? Ni tunanin wannan yarinya nakeyi da mummynta, ya zamuyi dasu?"

Sister sajida tai numfashi tace "allah sarki, yaya wlhy inaga nafika damuwa kan ciwon mami, ga yarinyar nan jawahir vatada wani sukunin daya wuce ta ga mamarta rasamu Ify, ga kuma abunda ya faru? Tsoro na daya kada mami ta mutu bansan ya jawahir zatayi ba, yarinya me nitsuwa"

Da sauri ya dago kai yace "noo sajida, bazata mutu ba insha allahu, zata samu Ify, ko dan samarwa jawahir farinciki ma,i have to do everything". Sister sajida tace " meaning what yaya shahid?" Yace "yes, i mean ko k'odata za'a sawa mahaifiyar jawahir dan ta samu Ify". Sajida tace "yaya? Da gaske kake😳?"

Yace "yes, i mean my words, inason maminta tasamu Ify sbd inason tasamu kwanciyar hnkln da zai bani damar bayyana mata taimakon da nakeso tamin ". Tace "wani taimako yaya shahid?"

Yai murmushin k'arfin hali yace *"kamar yadda kika sani, inada matsala sosai da zuhra gashi dad sun hanani in rabu da ita, ita kuma ta kasa sauyawa, kuma ni bazan iya bijire musu ba, shiyasa zan kai musu zabin raina nima yanzu, inaso in ji dadin ryw kamar yadda kowa ke ji, inaso insamu so da k'auna irin wadda kowa kesamu from his wife, meaning jawahir ta mini inaso in aureta in rayu da ita sbd na yaba da hnklnta"*

Sister sajida tace "u mean kanason ka auri jawahir yaya shahid😀?". Yace "yes, ko ba ta dace dani ba?😉". Tai saurin cewa "a'a wlhy, dadi kawai nakeji na mgnr, wlhy kun dace da juna fiye ma da aunty zuhra" Nan da nan ya canza fuska yace "ki barmun mgnr ta please sajida in baso kike mu b'ata ba"

Da sauri tace "ayi hkr yaya, amma kanajin dad ze yadda kabawa mami k'odarka asamata, more especially ma in yaji kanason yarta ne?". Yai shiru daga bisani yace " ba yadda za'ayi dad ya yadda sbd na fuskanci dad na fifita son zuhra a ransa fiyeda ni wai duk sbd zumunci, amma insha allah zan san yadda zanyi handling abun sbd bazan fada masu inason jawahir ba se bayan anyi ma mami aiki angama"

Sister sajida tace "toh allah ya temake mu, kuma yasaka maka da alherinsa"

Haka sukayi ta tattaunawa kan jawahir

•••••••••••••••

Ita kuma jawahir bayan sajida ta fita aka bugo mata waya, tana dubawa taga lambar nabila, ta daga suka gaisa, nabila tace "sistoo wai me ya faru ne tsakaninki da yaya mus'ab? Ya hana mu kiranki yahana mu amsa wayarki ko kin kira, rannan yaduba wayar hanifa yaga cikin call logs mun kiraki, yayita fada wai kada mu kuskura, kuma lkcn ma wayarki a kashe, yaune kawai muka buga muka sameki, gashi shekaranjiya shida big bross sun kwace wayoyinmu, mun rasa yadda zamu nemeki shine mommah tace muje gidanku, mukaje kuma akulle ba kowa, a layin gidanku muka yi clear dashi shida wannan k'awarki nana wai zatazo gunki ne ya kawota, nan

ma seda ya sab'a mana daya koma gida"
Kukan jawahir ne ya katse nabila ba dan ta gama ba tace " aunty jawahir meyene kuke kuka? dan allah ki fadamun?". Jawahir tana kuka tabawa Nabila Ibrn komai, sosai Nabila taji haushin abunda d'an uwanta yayi duk da cewar tasan ba Ify ba dan taji tadin mommah da mummyn mus'ab kan halin hjy Rahanatu mamar Nana kenan.
A hnkl take bawa jawahir hkr on behalf of her brother, sannan daga bisani ta tambayeta awani asibiti suke, jawahir tace " muna doctor shahid ne" nabila tace "insha allahu zaki ganni anjima, ki k'ara hkr dan allah Aunty jawa kinji?". Jawahir tace "Nagode da kulawarku nabila, u nd hanifa means alot to me amma alak'a ta daku bazaisa ku bijire ma d'an uwanku ba sbd shine gaba daku, kuma ni daku munsan juna ne a dalilinsa, abunda nake nufi shine kiyi hkr kibi umurnin yayanki kada ki sab'a masa a dalilina"
Sosai jawahir take nunawa nabila tabi mus'ab amma Nabila tace "wlhy ko ya mus'ab ze kashe mu se munzo gunki mun duba mami, mu ba ruwanmu ko da ace kinyi masa wani abune ma ai wannan tsakaninku ne, Bare ma kuma baki masa komai ba, kawai tsabar munafurci ne na Nana, kuma insha allahu bazatayi tasiri akanki ba"
Hawaye ne masu zafi ke sulalowa a fuskar jawahir, tace "dan allah kibar fadawa nana haka, har yanzu inason Nana, inajinta araina matsayin da take a baya, kada ki aibata ta, in ma wani abun kikaga tayi kiyi maba fatan shiriyar allah kinji?"
Shikenan aunty jawa "Allah ya bawa mami Ify"

••••••••••••••••••••

_TATTAUNAWAR MOMMAH DA MUMMY_

Mommah tace "kina nufin Rahana k'awar ki ce?". Mummy'n mus'ab tace " Tabbas Rahana k'awata ce amma abaya tun lkcn da mukayi secondary skul da ita, har nayi aure muna tare, se bayan nan ne muka rabu da ita, dalilikuma shine, mun saba da juna nida ita kwatsam tazomin da mgnr banza bayan bikina da sati daya wai tanasota auri mijina sbd kadamu rabu mucigaba da gudanar da rywrmu har mu mutu tare,......"
Mommah tace "dirk'ashi! Ke kuma gaki dason mijinkin nan kanar shine autan maza, zanga ya za'ayi😆". Mumny tace "a'a mommah ai kema sanin kanki daddy'n mus'ab bashine autan maza ba amma dai yafi kowani namijin dake ryw yanzu a duniya😊"
Mommah tace "toh inajinki , ya kukayi?". Mummy tace " na nuna mata wannan mgn ba mai yiwuwa bane, taje tanemi mijinta nima narike nawa mijin zaifi mana zaman Ify, muna cikin wannan tadin se ga daddy'n mus'ab yadawo da yaronsa zai bashi wasu kudade zayyi masa sayyayan kaya a dubai, danaga sunshigo senaja mijina daki, na fada masa abunda nana ke cewa kuma nafada masa kada ya Mata fuska, to ashe tashin danayi itakuma ya mata dadi sbd tasamu ta gana da yaron mijina wato alhaji lawan, se da takoma gida sannan tamun waya wai tunda banason zama da ita toh ta ga mijin aure a gidana, kuma ya mata dan hk dole muyi shige da fice itama tasamu ta haye kamar yadda na haye, da na tambayera wani irin hayeqa se tace zatazo tamun byn in an kwana biyu, bayan kwana biyu datazo take cewa wai ai sunyi exchanging number amma be samu da kiranta ba. Kullum itace me kiransa shine ita yanzu

abunda takeso inzo inmata rakiya gun wani malami dan a kama mata alhaji lawan a hannu, ni kuma nanuna mata ba ruwana se tayi tfyrta, daga wannar ranar bata sake kirana ko lekoni ba se randa tazo takawo min invitation card ko zama batayi ba wai adole tanajin haushina sbd banasonta da alkairi. Nikuma gara hkn ma sbd nagane ita ba abokiyar zama bace tunda ga hanyar data kama nabin malaman tsibbu, kuma ko ba komai ma gara datayi auren tunda bazata mannewa mijina ba, Can musu itada lawan din, kinji abun da ya hadamu da Rahanatu daganan muka yanke hulda, amma lawan har yau ana tare"

Mommah tace "aikuwa mus'ab d'inma ta lawan d'in akai masa ga dukkan alamu". Mumny tace "hkne, kuma nikam ba zan bar dana ya auri jinin Rahana ba dan bazan zo ina ganin jikokina na bin gidajen malamai abayan gari ba, yanzu meye abunyi?". Mommahtace " shirya yakaimu gidan nasan ya za'ayi"

_GIDANSU NANA_

Da gudu ta fito tana cewa "my darling kaine da kanka da rana ranan nan haka? Baka tunanin rana ze kod'ar mini kai neh?". Nana kenan sanye da wani material riga da skirt kanta ba ko d'ankwali, Ko kallon inda su mummy da mommah ke tsaye batayi ba, mus'ab ne yace "Nana kanki ba dankwali bakya ganin mummy na neh da mommah a wajan?"

Ta juyo ta kallesu tace "Oh sannunku da zuwa, mummyn ja ne wannan d.'in darling, naganta cikin hijab se naga batayi kalar aceitace mummyn kyakyawan saurayi kamar ka ba".

Mummy tagama fusata tace "eh uwar kice inaga ta haifamun kyakkyawan saurayi din , tunda ke hujabi batakai ta haifeshi ba se me yawo da tsiraici awaje koh?" Tajuya takalli mus'ab tace "son, wannan abun ce abunda kake k'auna kake fatan ka aura? Kake burin ta haifa ma yayanka? Dubi fa jikinta?"

Yace " mummy kiyi hkr, Nana fa batasan ke vace shiyasa, nine me laifi da ban sanar mata zuwanku va"

Momnah ta doka salati ta juya kan nana tace " ke kije ki k'ira mana uwarki, ba munzo kallonki da mad'enki bane, gun tsohuwarki mukazo, kin tsaya kina binmu da idanu". Nana sumu sumu ta juya ta dawo tareda mum d.'inta tana cewa "bari na kawo musu abun sha"

Mum d'in nana tazauna tana binsu da idanu, mus'ab ya gaisheta, sannan ta juta ta kalli mamarsa tace "sannunku da zuwa, ya hanya?"

"Lfy lau," mommah ta amsa mata, mumny kuwa cewa tayi "Rahanatu banajin kin manta ni. Ina kyautata zaton kina tune dani, kuma kinsan koni wacece, wannan da mus'ab kinsan nice na haifesa, kuma kinsan nasan ko ke wacece koh?"

Nan da nan mum din nana tasha jinin jikinta, tace " meya iawo dogon bayanin nan hjy? Yanzu fa nidake jamata yayi muhada kai tunda taranmu sun dedeta saura mgnr aure"

Mummy tayi murmushi tace "kinyi saurin karaya ai Rahanatu, dan kawai nace nasan ko ke wacece? Toh ki kwantarda hnklnki ba tone tone nazo yi dakeba, nazo ne in gargadeki keda wannan yarinya taki marar kamun kai, da ku fita hanyar mus.'ab, ku kwance kulle kullen da kukayi akansa domin bazan Taba yadda dana ya auri yarki ba"

*••••••••✍ by Sajnaa*
*08140813180*

[6/1, 12:10 AM] Sajna: . 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajnaa*

*56↗60*

Basu jira tace komai ba suka mik'e, mys'ab jikiba k'waei yabi bayansu, suka ja moto suka bar mum din Nana da tunani.

Bata tsaya bata lkc bata dannawa hjy shabuki waya, batan tagama wayar ne Nana ta kalleta cikeda damuwa tace "mumcy yanxu meye abunyi? Kinsan idan na rasa mus'ab kamar na rasa rayuwata neh"?

Rahana tace "dont worry my baby, ba abunda ta iya, ai dan nata ba jawoshi mukai ba shiya kawo kansa dan hk ba ta isa ta hana auren nan ba"

Mommah da mummy ransu ya gamab'aci sbd yadda mus'ab yayita misbehaving akan Nana, abun be musu dadi ba kuma mummy'nsa ta fada masa gara yacire ransa dan in har tana numfashi bbu shi babu Nana, sosai abun ya dameshi amma ba yadda ya iya she is d one whu gave birth to him kuma ta rene shi tun kafun ma yasan kansa bare kuma Nana.

_Dr shahid clinic_

Aaseey white ne ta bugowa jawahir waya, cikin fara'a ta amsa tana cewa "amarsu bakya laifi, k'amshin ki nakeji ta cikin wayata".

Aaseey tace "halinki na nan jawahir". Jawahir tace "ya kike?".

Aaseey tace "Ify lau, kin san muna k'ofar gidanku yanzu hk nida me house dina? Munzo kuma gidan arufe, munje anguwa nace mubiya mu duba ki gashi ke kuma bakwanan, Nace bazai wuce kina gidan rabin ranki Nana ba sbd ita ce kika damu da ita akanmu"

Sosai jawahir taji ranta ya sosu sbd yanzu sunan Nana tanajin sa newith a dfrnt sound ko a bakin waye yafito, tai murmushi tace "a'a ba gidansu nana najeba wlhy, mami na ne take asibiti kinsan batada cikekken Ify ai, toh ynz za'ayi mata dashen k'oda ne". Aaseey tace "allah sarki mami, allah yabata Ify, wane asibiti neh?"

"Dr shahid clinic" jawahir ta bata amsa a tak'aice. Aaseey tace "toh muna zuwa ynz inshaa allah"

"Toh allah ya kawoku"

Tana kashe wayar sister sajida tashigo itada su Nabila da hanifa, tace "jawahir ga wasu

suna nemanki nan"
Suka gaggaisa tana zaune tana kallonsu, mami kuma anyi mata allurar bacci se bacci takeyi, nan su Nabila da hanifa suka shiga bawa jawahir hkr ita kuma hawaye kawai ke sulalowa, hankalin sister sajida yatashi dan batasan kan zancen ba, kama zatayi mgn se ta fasa, sbd ba dadi wani bayaso in bai saka a lamarinsa ba ka shiga, se ta yanke shawarar zata tambayi jawahir din in sun tafi.
Hanifa tace " aunty jawa ki kwantar da hnklnki kada ki damu, insha allah yaya mus'ab is urs, bazai taba zamowa mallakin wata ba, insha allahu komai ze daidaita tunda mummy tazo gombe yau"
Nabila tace " yes, mummy tazo kuma mummy tana side dinki ne tace ke takeso as surukarta ba Nana ba".
Jawahir tashare kwalka tace " ba komai, duk abunda allah ya rubuta se ya faru da bawansa, wannan jarrabaw tace kuma kaddarata ce, ko da mus'ab be aure ni ba bazan tab'a blaming Nana ba sbd duk abunda ya faru ga bawa toh maliccinsa neh ya tsar masa hkn, kuma allah ha azzalimi bane ga bayinsa, dukkanmu mu dogara a garesa se mu samu tsira duniya da lahira, nikuma ku tayani addu'a allah yabawa mami na lfy, daga nan nikam.komai ze daidaita sbd lfyr mami tafimin komai, koda duniya da abunda ke cikinta aka bani aka tauye lfyr mami na, zan hada duniyar duka don na fanshi lfyrta"
Ta share hawayen fuskarta, suma duka hawaye ne a fuskarsu, ta k'ak'alo murmushi tace "ban tambayeku ba, ya mommah da mummy din suke?".
"Lfy lau," syka amsa mata.
Tace "ku gaidasu in kun koma"
"Insha allahu zasuji, zamu koma, allah ya k'ara sauk'i"
"Ameen"

Ta rakasu tadawo tasamu sister sajida na gyarawa mami kwanciya, ta zauna tace "sannu da kokari sister sajida, allah ya biyaki da alherinsa"
Sister sajida tayi murmushi tace "Amin allah ya biyamu dukanmu😊"
Tazo ta zauna close to jawahir, ta rik'e hanunta tace "niko tambaya zAn miki in bazaki damuba?".  Jawahir tace "ji sister sajida harda wani cewa in bazan damuba, toh wani tambaya ne ma zakimin har Yasa in damu? Ki tambayeni komai kanki tsaye"
Sister sajida tace "ok, dan allah su waye wadannan yan matan? meye alak'arki dasu? Hak'urin me suke baki har yasaki kuka? Waye mus'ab da nana? Kuma meyene yake faruwa tsakaninki dasu?"
Jawahir tace " wadannan sunansu Nabila da hanifa, k'annen mus'ab ne, mus'ab kuwa shine namijin da nake jin babu tamkar shi yanzu a duniya, he loves nd care lyk a mum, Nana kuwa aminiyata ce wadda mutane da yawa ke kiranta rabin ran jawahir, nima kuma ana kirana rabin ran Nana"
A hnkl jawahir tagama bawa sister sajida lbrn komai bata boye mata ba, hawaye ne a fuskarta haka sister sajida ma, a hnkl ta rarrasheta tace "insha allahu komai ze wuce, duniya dama hk take, zakaga abubuwa kala kala in dai baka mutu ba"
Aaseey white ne ta bugo waya tana tambayar jawahir dakin da suke, jawahir da sister sajida suka dunguma suka shigo da aasey white, bayan sun gaggaisa tayi musu ya me jiki ne take

cewa jawahir "ya Ibrn bikinki?"

Jawahir tace "anata shiri". Aaseey tace "NANA kuma fa? Tace mun seta samu choice d'inta zata sanar dani amma shuru nakeji"

Jawahir tace "nima banji Ibr ba, tun kan uncle aarif data ce bataso"

Aaseey tace " Nana ba mutunci ai, yadda bawan allah'n nan ya sota kamar ya mutu amma ta walak'antashi, bari na kirata"

Tadanna kira se taji ana ce mata kudin ta sun k'are, ta kalli jawahir tace "yanzu fa abakin asibiti nasa 500 ke kadai na kira amma har sun debe, lalle mtn b'arayi ne, bani wayarki in kirata in akwai kati"

Jawahir TAa mik'a mata wayar, ta danna lambar nana yayi apearing da suna *_MY UNIQUE_*.

Aaseyy tace "hada wani my unique koh?mu kuma ko oho? Bansan meyasa ba jadamu dake ko damuwa dani bakiyi ba, dan naga sunan da ake kirana a skul kika samini wai aaseey white amma nana harda saka mata unique, dan dai ke ba namiji ba ne amma da se nayi fada da nana akanki sbd kinayi mana warayya kinfi fifita sonta akaina"

Jawahir ita kanta tasan aasey nasonta sosai, duk cikin k'awaye aaseey ta daban ce, duk da kasancewar ta yar masu kudi amma sonda takewa jawahir ko yar uwarya iya kaci, se de jawahir kuma tariga ta shaku da Nana sbd tun primary suna tare shiyasa kullum aaseey cikin k'orafi takeyi, jawahir ta danyi murmushi tace "am sorry my aaseey, accept my apology, kema ai inasonki kuma na damu dake sosai da sosai, kuma insha allahu kema zan saka special name flyeda na NANA"

Aaseey taji dadi sosai tace "ko kefa? Yanzu ne zamu daidaita bari na kira nana , kinga me house yanacan moto arana"

Ta danna kira tasa hands free dan tanso ta tsokaneta da cewar ya uncle aarif, se da ya kusan d'aukewa sannan Nana ta amsa tana cewa *_WAI MEYENE KIKE KIRANA DA TSAKAR RANA? IN MGNR MUS'AB NE FA KISANI BANI NA KAWOSHI BA SHI YAZO YACE YANASONA MUYI SOYAYYA DAN HK KIJE KI KIRASHI KIMASA KORAFI, SE DE INDA ZAKIBI SHAWARATA RASHIN KIRAN YAFI MIKI SBD IN KIN KIRA SHI MA ZAKIJI BA DADI,SBD YANZU AM D ONE RULING HIS HEART NOT U, NICE NAN MATAR MUS'AB KO ZAKI MUTU, DAMA BINKI NAKE DA IDANU INA GANIN TAKUNKI, KAFUN NASAN HANYAR DAZAN B'ULLO MIKI, ALHAMDULILLAH HAQATA TA CIMMA RUWA, NA KWACE MUS'AB A HANNUNKI KAMAR YADDA AKE KWACE ALEWA A HANNUN YARO, KEDA MUS'AB SE HANGE DAGA NESA SBD DAMA BAKI DACE DASHIBA, KINSAN ANCE K.'WARYA TABI K'WARYA, KINGA KUWA BA YADDA ZA:AYI A HADA YAR TALAKA DA DAN GIDAN MASU WADATA, WANNAN EQUATION NAKI BAYYI BALANCING BA, SE YANZU NA SAMAR DA BALANCED EQUATION_*

Karaf ta katse wayar, aaseey tajuyo tana kallon jawahir cikeda mamaki, jawahir kuma hawaye ne ke sulalo mata, sister sajida tashare mata hawayen tayiwa aaseey white bayani yadda jawahir tayi mata.

Aaaseey tace "abunda Nana zata saka miki dashi kenan jawahir? Duk yadda kika daukaketa akan sauran kawayenki?"

Ta xauna suka gaisa ya kawo mata drinks tace "ina mutumiyar?".
"Tana chiki, bari na kirata."
Tace "wait, bari in tambaye ka, an samu progress kuwa a alak'ar ku? Dan nagan ka somehow kmr hnkln ka ba a kwance ba."

Yai murmushin pretendance yace "eh alhmdllh, ke da mami kun kyauta."

Aaseey tace "u'um mus'ab gayamun gskia, alhmdllh da ka fad'a baxai wadatar ba sbd kowani musulmi yake ciki godiya ga Allah tilas neh."

Yai ajiyar xuciya dan besan ta ina xe fara fad'a mata xaman doya da manja sukeyi still ba.

Tace "mus'ab feel free nd talk to me, Banida kmr Jawahir a k'awaye hkne itama ynx batada kamar ni, dan hk ka yadda dani ba ina neman jin sirrinku bane."

Yai murmushi yace "habaa maman twins ai ba xancen rashin yarda anan, kawai banason abunda xe had'a princess da mami neh."
Tace "ok, na ganeka mus'ab, kafiso kayita cutuwa sbd ka faranta mata tayi yadda takeso knan? Dis is not gud, she's ur wife, dole tayi maka biyayya."

Yai murmushi yace "Hmmm, Maman twins kenan, ina kika baro twins?"

Tace "suna gidan mummy na tun safe."

Yace "lalle yau baxaku shirya da mutumiyar ba tunda baki taho mata da yaranta ba, bari na kira miki ita."

Aaseey tai murmushi kawai ta bisa da idanu, aranta tace "Ayya mus'ab."

K'ofar Jawahir yafara knocking, Aaseey ta na jiyo muryar jawahir lkcn da tace "meye ne kake min knocking a k'ofa?".
Yace "maman twins ne taxo."
Da sauri Jawahir tace "da gaske?"
Yace "Eh mana, tana parlour."

Aaseey tana jinsu kuma tabbas taji haushin yadda Jawahir ke yiwa mus'ab magana ba girmamawa.
Dan haka dole ta gwadawa jawahir kuskuren ta.
. batayi wata wata ta mik'e ta bar gidan.

Mus'ab ne biye da Jawahir suka sauk'o daga stairs d'in, amma wayam suka gani, ba Aaseey ba alamarta.

Jawahir ta kalli mus'ab tace "ina take anan?"
Yace "nima tmbyr da nake yiwa kaina knan."

Jawahir tace "in bata xo bane ka fad'amin na koma nayi kwanciyata."
Yace "wlhy Aaseey taxo, kuma ni na taho na barta a falon nan nace bari na kiraki.".

Jawahir mamaki ya isheta, suka gama lek'a duk wani corridors na gidan ba Aaseey dole suka hak'ura, mus,ab ne ya nufi gateman ya tmbye shi.
Gateman yace ai ta fita yanxu kuma yaga ta tari keke napep ta shiga.

Mus'ab yai ajiyar xuciya yace "Allah yasa lfy."
Ya dawo cikin gidan.
Direct d'akin Jawahir ya nufa ya shaida mata yadda me gadi ya fad'a.

Itama mamaki take toh meyasa Aaseey ta tafi? "Toh" kawai ta ce masa.

Yana fita tafara kiran lambar Aaseey, cikin rashin sa'a taji wai unavailable.

Aaseey kuwa gidan mummy'nta tabi tad'au Twins suka koma gida.

Mijinta yace "gimbiya ya naga kundawo da wuri haka?"

Tai ajiyar xuciya tace "hmm jawahir batada dama wlhy."
Yace "aaah! Yau keda Jawahir kuma? Dama akwai randa xa'aji kanku neh?"
Tace "hmm kai de kabari, amma wlhy tabbas Jawahir tanayin abunda be dace da ita ba.."
Yace "meya faru neh?"
Nan ta labarta masa komai. Shima ya jinjina abun.
Hak'uri ya bata yace "a hnkl xaki nusar da ita kinsan batada kamar ki."

Tai murmushi tace "dat's my husband,inajin dad'in yadda kake bani shawarwari akan al'amurana, tnx yhuu so much."

°°°°°°°°°°°°°°

One week later.

Aaseey a gidan mami.
Wayar mami ta d'auka ta fara typing text message, se data gama sannan tayi sending wa Jawahir.

Jawahir kwance take taji wayarta na beeping, Ta d'ago da sauri taga lambar mami ne, ta bud'e sak'on kmr hk.

_Auta kin kyauta abunda kikayi, ashe duk fad'an da nayi miki baki d'auka ba koh? Yayi kyau, tunda ban isa in fada kiji ba, ki cigaba da yin yadda kikeso d'in yana da kyau, kada kiyi tunanin bansan abunda ke faruwa a gidanki ba, toh Aaseey taxo ta fad'amin komai, kuma nagode da kyau._
_Sannan kada kiyi tunanin xuwa guna tunda bakijin maganata, kije gun wanda kike jin maganar sa ki d'aukeshi a matsayi na._

Ido taxaro tace "na shiga uku nah? Meye nayi har Aaseey ta fad'awa mami?"

Aaseey kuwa tana ganin ya shiga ta goge sak'on daga sent messages, ta cigaba da sha'aninta..

Lambar wayar da shahid ya kira mami dashi lokacin biki yayi mata murna, shi Aaseey ta k'wafa a phone d'in ta sbd tsaro.

Bata wani xama bata takoma gidan ta.

Jawahir kuwa duk hnklnta ya tashi tarasa yadda xatayi da ranta.

Sak'e sak'e take tayi koh mus,ab ya fadawa Aaseey wani abune ta fad'awa mami?

Wannan kenan.
••••••••••••

Bayan kwaba biyu.

Aaseey ne ta dakawa jawahir sammako, ko da ta shiga gidan mus'ab ne yake cire takeaways daga cikin wani leda yana jerawa a dining.

Ta watso masa kallon keye haka, yai murmushi yace "barka da  xuwanko dai aminiyar mu."

Tai kim sannan tace "mus'ab gaskia sakalcin jawahir harda laifinka sbd ba haka take ba agidan mami, ita keyin komai, bayan akwai masu aiki anan kuma ace girki ma baxata iya yi makaba?"

Yai murmushi yace "K'awarmu kenan, ke ma kinsani k'awar takin sai a slow."

Ta nemi guri ta xauna tace "k'arfe nawa?"

"9:38" yabata amsa a tak'aiche.
Tace "bacci ne takeyi?"
Yace "bari na duba." Ya haura sama.

Direct d'akon ya tura, yayisa'a a bud'e ne, daidai fitowar ta a wanka kenan da tiwel a jikinta.
Ta watsa masa kallo tace "Ify?"
Yace "Aaseey tana parlour tana jiranki."
Be jira amsarta ba ya fito, da sauti jawahir ta sauk'o xuwa k'asa.
.

*Sajna ce! Mrs Abdul.*
[6/1, 12:14 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*161↗165*

Jawahir tani jawahir da kallo sannan ta sauk'e idanunta.
Jawahir ta xauna kusada ita tana cewa "nagode wa Allah daya kawomin ke."

Aaseey tace "na me knan?"
Jawahir tace "bansan me nayiwa mami ba se gani nayi ta min msg wai tagode tunda banajin mgnrta, a k'arshe kuma tace ke kika fad'a mata komai."

Aaseey tace"toh kinga laifi na neh? Ai wlhy inde gskia xan fad'a miki wlhy bakya kyautawa mijin ki amma ba komai tu da hk kika xab'arwa kanki, ni ynx haka ka in badan dalili ba ba ganina xaki yi a gidanki ba."

Jawahir ta dafe k'irji tace "na shiga 3 wai me nayi neh.?"
Aaseey ta cito phone dinta ta fara dialing number doctor shahid, har ya katse ba'a amsa ba, yana yankewa se ga kiransa ya shigo, ta amsa da sallama suka gaisa tace "halinka yana nan, baja amsa wayar mutum sedai ka kirasa, toh dama akan mgnr da mukayi ne, ynx hk ina gidansu, gata kuyi magana."
Bansan me yace mata ba se ji nayi tace "toh bari na bashi."

Ta mik'awa mus'ab wayan tace "Ga doctor kuyi mgn.".
Da sauri jawahir ta mik'e xata wafce wayar, Aaseey tace "meye hkn?"
Mus'ab ya gaisa da doctor. Daga bisani doctor yace "da farko inayi muku murnar biki, Allah yabaku xaman lfy da yara nagari, sannan dama munyi mgn da Aaseey ne akan abunfa jawahir ke maka shine tace koh xanyi mata mgn, shine yanxun nace ta baka phone d'in mu gaisa in kuma baka hak'uri kuma in nemi ixinin ka inka amince muyi mgn da jawahir d'in."

Mus'ab yace "nagode sosai, ka kyauta min, kuma komin kishina ban isa hanaka mgn da jawahir ba, dan hk u're free."
Ana bata wayan ta fashe da kuka, tana cewa "shahid dama kana tine da ni? Ka manta da rywta na tsawon lokaci haka? Shahid meyasa ka yi min abunda kayi?"
Da k'yar ya lallab'ata tayi shiru daga bisani ya d'ora mata da nasihu masu shiga jiki da xuciya.
Cikin kuka tayi masa godiya sannan ta tmbyesa yaushe xaidawo nigeria, yace mata se in taji mgnrsa tukunna.
Aikuwa tace "insha'Allah doctor nad'au mgnr ka baxan sake yin abunda be dace ba."
Yace "toh shikenan jawahir, ina miki fatan alkairi, allah ya albarkaci rywr ku."
Kuka sosai takeyi lkcn da tayi sallama dashi, daga nan kai tsaye d'akinta ta koma ta haye gado tashiga rera sabon kuka.
Aaseey kuma daganan ta tattara tayi tafiyarta, ta koma tabawa mami lbrn komai, mami tayita mamakin al'amarin jawahir, tace "toh allah yasa da gaske takeyi."

Aaseey tace "amin, ai in ankwan biyu xanje nagani ko ta sauya."
Mami tace "toh mungode allah dai ya k'ara miku albarka."

❣❣❣❣❣❣❣

*6 months later.*

Gidan tsaf tsaf kmr yau aka faea shigansa, haka k'ayataccen falon gidan ma, jawahir na hango tace kwalliya cikin leshin pink colour ta kashe d'auri tana sauk'owa daga step, a hnkl take takun har ta iso.

Nikam.ido nake binta dashi kmr ban taba ganinta ba, dining ta nufa inda naga mus'ab xaune yana karyawa.

Da sauri taja kujera ta xauna tana cewa "meye.hkn xakaci abinci da kanka, toh tunda ynx kam.na fito se ka ban spoon d'in na ciyar dakai."

Na gwalalo idanu cikeda mamaki, inda naga mus'ab ya biye mata se wani lobewa sukeyi abunsu.

A haka suka gama karyawa se wani nan nan suke da juna, direct falon suka koma suka xauna suna kallo, Jawahir tasaka k'ara tana rik'e cikinta, da sauri mus'ab ya tallafota yana yi mata sannu, ta bud'e idanunta tana kallonsa, yace "sorry maman baby, baby ya na miki naushi koh?"

kai kawai ta d'aga masa, yace "sorry once again, yadda baby ya wahal.min da ke nima insha'Allahu xan rama miki in yaxo duniya, se nayi masa bulala fiyeda naushin da yake miki."

Tace "me sunan doctor'n xaka daka kuma?" Ta had'e rai.

Yace "sorry princess, wasa nake miki, ai me sunan dr, ko wani naga ya tab'a mana shi se inda karfina ya k'are."

Tai murmushin jin dadi, yasa hanunsa yana shafar cikin ta.

*Sajna ce.*
[6/1, 12:14 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*166↗170*

Xuwa ynx hnkln kowa ya kwanta, jawahir tana kulawa da aurenta yadda ya kamata.

Yau da yamma Aaseey ne takawo mata xiyara, bayan sun gaggaisa se ga mus'ab ya dawo.

Jawahir ta mik'e tashiga hidimar mijinta ba kama hanun yaro, Aaseey ta gwalalo idanu taba kallonsu.

Jawahir tace "Maman twins wannan irin kallo haka?"

Aaseey tace "hmm toh me xance? Ai gani nayi abun naku yanaso yafi k'arfi na ne.".

Jawahir tace "Ku fa kuka ce in kula da aurena, yanxu kuma kunfara complain?"

Aaseey tace "ba complain bane kawae dai ina mamakin kine."

Jawahir tace "toh kirufe idanunki malama, ki bar saka mini idanu nida mijina."

Aaseey tace "da kyauuu."

Jawahir ta kyalkyale da dariya, ta cigaba da bawa mus'ab d'inta abinci.

💟💟💟💟💟💟💟

_Nana_

Duk abun duniya ya dameta, ta rasa me ke mata dad'i, batajin xata iya barin Jawahir ta rayu da mus'ab sbd basu dace ba, dan hk duk wani hanya da xata bi ta rabasu se ta bi.

Wannan tunanin ne ya hanata xama se kai kawo takeyi a parlour, wani murmushi tA sake da alamun ta samarwa kanta mafita.

Waya naga ta d'aga ta kira wani nomba, tace "hello d boy inason ganinka a gidan old man d'ina anjima."

Tayi hanging ya cigaba da murmushi.

Jawahir da mus'ab suka fito daga moto, hannunsu rike da kanyan shopping bags na sayayyar baby, wanda a scanning aka sanar musu namiji ne, yamxu ma daga asibiti suke, sunje anduba musu lafiyarsa sannan suka wuce wajen sayayya.

A parlour suka baje suna hutawa.

Aaseey ylta bugo waya cewar da yamma tana xuwa.

Jawahir tace "toh se kinxo, gashi munyi ma little doctor shopping se ki xo kiganu koh?"

Aaseey tace "toh se naxo d'in."

K'arfe 2:30 mus'ab ya shirya xaije gidansu mommah ya d'auko Nabila taxo ta ringa kula masa da maman baby'n sa har xuwa san da xata haihu.

Murmushi yayiwa Jawahir yace "maman doctor ya naga kin had'e rai?"

Tace "banaso ka tafi wlhy, ka xauna kawai se inyiwa nabilan waya taxo."

Yace "toh ai se na fad'awa mommah, kuma kinga rabon da naje gidan mommah fa kwana uku."

Tace "kawai ni wayo xakamin habibi."

Yace "sorry princess, ba Aaseey'n mu xata xo anjima ba? Kinga se ta tayaki hira koh?"

"Nikam kawai banaso katafi ka barni ni 1 a gida, se dai mu tafi tare."

Yace "A'a princess banaso kisha wahala, kinga yau na rana, kuma nayi alk'awarin daga fitan da mukayi yau se kin haihu sannan ki sake fita."

Ta xaro idanu tace "se na haihu? Da yawa fa ya saura."

Yace "ba wani yawa one month kam kamar yau ne."

"Tabb  nikam baxan iya one month banga mami na ba."

Yace "kinaso kiringa wahal da little doctor'n mu knan?"

Tace "a'a, ai ba xanyi abunda xe tabamun baby ba."

Yace "toh in hkne u must stay at home abeeh?"

"Ok, kasayo min chocolate a hanya."

"Ok bye, i love yhu enermously."

Tai murmushi tace "luv yhu too habeeby."

Ya matso close to her ya manna mata kiss a kumatu💋.

Ta rik'e jikin rigarsa tana jan phone dinsa yace "wat?"
Tace "selfie mana habeeby, kayi kyau sosai."

Ya mik'a mata phone dinsa ta kashe musu selfie, sunyi kyau sosai ganin sha'awa.

Har bakin motonsa ta rakasa sukayi bankwana ya tafi. Murmushi takeyi sosai kuma se hawaye yabiyo baya, ta share da sauri ta shige cikin gida.

Tana komawa ta kira Aaseey.
"K'awa ya bakixo ba?"

"Kai, yaushe yamman yayi ma?"

"Dan allah kixo dàwuri nikam, kinga habeeby yatafi ya barni ni 1 agidan, duk bbu dadi nakeji."

Aaseey tace "xanbi gida inkai twins gun mummy na fa."

Jawahir ta ce " dan Allah kitaho dasu mana Aaseey, nifa xaman gidan ne banaso ni 1."

Aaseey tace "kijimin jawahir dai, se kace kullum.bake 1 kike xama ba."

Tace "Haba mana Aaseey, in kinxo ai xamu d'anyi tad'i da yawa kafun magriba."

"Toh shikenan, bari na shirya yanxu naxo, amma twins tun wankan safe ban sake yi musu ba, kuma nanny'n su akwai sand'an aiki, dan haka kwasosu kawai xanyi kiyi musu wanka."

"Eh na yadda, xanyi musu harda kwalliya."

Tayi hanging wayar, ta kunna tv tana kallon film d'in uzuri.

Ba jimawa bacci ya d'ebeta, kawai jin muryar mutane tayi akanta.

Aaseey kuwa da kanta take driving moton da mijinta ya sai mata range rubber red colour, a k'ofar gidan tayi parking sede mamaki ne ya kamata lokacin da taga motoci biyu a k'ofar gidan, a ranta tace jawahir na neman abokin tad'i gashi tasamu bak'i har moto biyu.

Kafun ta gama tunanin se ihun jawahir ta jiyo, bata aune ba se ganin k'attin maxa tayi sun fito da jawahir tana ihu suna janta.

Da sauri Aaseey ta fito daga motonta ta nufo wajensu tana cewa "ku su waye ne? Kuma meye had'inku da jawahir?"

Bata ankare ba se ji tayi an doketa, aka manna mata gum a bakinta kmr yadda akayiwa Jawahir aka jefasu a moto a ka ja moton dawani wawan gudu.

Twins kuma suna cikin moton Aaseey se wasansu sukeyi, basu san meke faruwa ba.

Sun kai 10 mins kafun su fara kuka a moton suna kiran mummy Daddy.

Wata black moto ne ta danno kai a kofar gidan, 'yanmata 2 dake ciki Nabila da Hanifa suka fito cikin takun gayu.

Moto suka gani a bud'e ga kukan yara aciki, da sauri sukayi wajen, suna lek'awa sukaga twins d'in Aaseey ne.

Nabila tace "Kamar yaran Aaseey white k'awar anty jawa koh?"

Hanifa tace "sune ma ai".

Nabila tace "toh me yasa ta barsu a moto a waje?"

Hanifa tace "waya sani? Gashi se kuka sukeyi, mu shiga dasu kawai."

Suka d'au babies d'in suka rufe moton suka shiga gidan.

Falon shiru ba kowa, mamakine ya kamasu, haka suka haura suk duba dakunan gidanma shiru, tsorone yacika xuciyoyinsu.

Nabila tace "wai meke faruwa ne a gidannan? Yara awahe a moto kuma cikin gida bbu kowa?"

Hanifa tace "muduba gateman ko xaisan wani abu?"

Direct d'akin gateman suka tura inda suka sameshi kwance kansa na xubar jini.

Wani wawan ihu nabila tasaka, Hanifa ma duk tsoritar datayi ta daurene kawai, ta toshewa Nabila baki tace "kada jama'a suxo ace mu ne."

Ta figo hanun Nabilan sukayi waje, motonsu suka shiga tareda twins d'in, hanifa taja moton a 360.

Se da suka bar area'n sannan ta yi parking a gefen titi ta kira yaya mus'ab.

_*Sajna ce.*_
[6/1, 12:15 AM] Sajna: . 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*171↗175*

A rud'e ta sanar dashi abunda suka tarar yace "wat?" Ta sake maimaita masa.

Mommah dake kusada shi tace "meya faru neh?"

A rikice ya sanar da ita ta hau salati, tana cewa, "bari naxo muje gidan, yanxu ina su Hanifan?"

Ta jawo hijab, suka fita, a k'ofar gida suka had'u da papa da big bross, ta sanar musu halin da ake ciki duka.

Dukansu sun shiga rud'ani, papa ya bugawa police waya ya sanar dasu, kuma ya musu kwatancen hidan mus'ab d'in.

Mus'ab yaja motonsa shida mommah, se papa da big bross ma a moton papa.

Basu jima da isa ba se ga moton police, su duka suka shiga gidan amma wayam suka gani kmr yadda suke tsammani, musa gateman kuma wani police ne ya tafi dashi asibiti.

Kusada wayar jawahir dake kan kujera sukaga farin takarda.

Mus'ab hanu na rawa ya d'auka ya fara karantawa kmr haka.

*_A bit suprised koh?_*
*_kada ka damu dan Jawahir da Aaseey suna safe hand in har kaso hakan, dan baxan cutar da aminiyata ba inhar ta kyautata amintar, sannan kuma baxan cutar da masoyiyar mijina ba, nan ma inta kyautata soyayyar._*
_*U hav 2 option.*_
_*Ko ka sake jawahir saki uku ka dawo dani.*_
_*Ko ka rasa rayuwar ta da wannan shegen d'an dake cikinta, dan haxan bar kowace mace ta haifa maka d'a ba a duniya*_

_*Idan kagama shawara ka nemeni, kasan nomba na.*_

_*It's no other person but me NANA.*_
_*BYEEE💁*_

Mus'ab besan sanda ya fashe da kuka ba, tunaninsa 1 kada nana.ta cutarda Jawahir da baby'nsa.

Papa ne ya karb'a takardar ya karanta sannan ya mik'awa police d'in dake wajen, dukkansu sunyi mamakin ache mace ne xata iya aikata wannan aika aikan.

Mommah cikin. Kuka tace "harda Aaseey ma? Itakuma me taci mata? Da xata had'a da ita?"

Papan yace "Ina yaran nata?"

Mus'ab cikin kuka yace " suna wajen Su Nabila."

Papa me yaita rarrashin mommah da mus'ab har sukai shiru daga bisani police d'in yace ina nombar Nana? Mus'ab dai guarantee bayida nombarta a kansa ko a wayarsa dan haka wayan Jawahir ya fara lalub'awa, ya gama duba names din da suka fara da N amma bbu Nana.
Se daga baya yatino name d'in da tasawa Nana tun suna skul, kai tsaye ya danna M se ga nombar Nana yayi appearing _*MY UNIQUE.*_

Ya d'auki digits d'in ya watsa a phone d'insa, ya mik'awa police din ma ya saka a nasa phone in.

Police d'in yace "insha'allah yanxu abu na farko daxamu fara yi shine mu san inda suke, kai mus'ab ka kira ta kaji, mu kuma xamuyi bincike ta hanyar network d'in dake aiki da lambarta.

A wajen yayi ta trying number'n ta amma switched off!.

Papa yace " Batada wani lamba bayan wannan kuma?".

"One sim take using, kuma da tanada wani lambar da na gani awayar Jawahir, papa wlhy ni damuwata 1 shine kada ta cutar dasu musamman ma Jawahir acikin halin da take d'in nan."

Papa yace "Insha'Allahu Allah yana gaba da ita, bbu abunda ta isa yi, ka kwantar da hnkln ka, yanxu abunda xamuyi shine mu nemi mijin k'awar tan mu sanar masa abunda ke faruwa."

Moton Aaseey dake waje suka duba, sunyi neman duniya bbu wayarta, dole suka hak'ura, gashi mus'ab bayida masaniyar wajen aikin mijin ta.

_*Nana.*_

Kid'a ta k'ure a moton ta se sharara gudu takeyi, wani gida naga ta shiga tayi parking ta fito.

Kai tsaye babban falon ta nufa inda ta tarar da k'attin samarin nan suna holewarsu da giya, ta watsa musu kallo, da sauri suka nitsu suna mata barka da xuwa.

Tace "ina suke?"
D boy yace "suna k'aramin room d'in can."
"Okey " kawai tafurta sannan ta haura d'akin.

Durk'ushe suke a d'akin dukansu bakinsu manne da manyan celetop, hannayensu d'aure da igiyoyi. basuda halin motsa bakin bare kuma magana.

Ta kyalkyale da dariya, kai tsaye cikin Jawahir ta kai hanunta ta shafa tace "wow congrats Jawahir, kinyi k'ok'ari wato har kin kusan ajiye masu tarwatsa jere?"

Jawahir banda hawaye bbu abunda takeyi, Ta juya gun Aaseey tace "Toh Aaseey white kike koh? Ina tabbatar miki very soon xaki dawo aaseey black dan ba ta dad'i xanyi miki ba, Sbd ina sane da duk hidimar da kikeyi akan xaman lafiyan mijina mus'ab da wannan shegiyar 'yar talakawan, ni a tunanina kamata yayi mu had'a k'arfi da k'arfe wajen ganin cigaba na sbd mune 1 mune masu abun duniya, talaka ba'ayi masa, ina tabbatar miki kinyi kuskure da kika canki jawahir akaina sbd a sannu xakiga illarta, muna nan wataran mijinki xe ce ita yakeso, kinga daganan ta tsine dake, Duniya da dukiyarsa ta xama nata."

Aaseey ta watsawa Nana mugun kallo a xuciyarta ta na k'ara jin tsantsar tsanar Nana da halayyarta.

Nana tace "wonderful har harara kike yi min? Da kyau, Aaseey taurin kanki yana burgeni tun muna skul ina fad'a miki haka, koda yake gara ke in kinyi ba laifi, ubanki na da abun hannu, wata kuma agidan k'osai da koko ta fito se xallan kanainaye miji sbd taga abun duniya.". Ta gama mgnr tana watsawa jawahir mugun kallo.

Celetop na bakinsu ta cire tace duk me mgn yayi, Jawahir cikin kuka take tmbyr nana "me nayi miki Nana da xaki sakamun da haka? Me na tare miki a rayuwa?"

Da sauri Nana ta juyo tace "Abu 1 kika taremin shine mijina mus'ab, in baki manta ba na fad'a miki mus'ab na da qualities da duk wata mace xata so shi. Tsiyarsa 1 bayida abun duniya, a lkcn da na fahimchi yanada shi kuwa se nabi hanya mafi sauk'i da xan mallakesa kuma na mallaka, amma daga baya yakoma hannunki, toh tabbas baxan barki ba se na k'wace mus'ab again daga hanunki kmr yadda ake k'wace alewa a hanun yaro, shashasha yar talakawa ona fatan kin fahimci me kika tare min yanxu?"

Aaseey tace "wallahy kin cika jahila kuma makira wacce bata k'aunar rahamar ubangiji, Nana gushewar ire irenku a duniya tamkar gushewar fir'auna ne wanda mutane da dama ke samun

sukuni bayan ranku, amma kisani Allah yana gaba dake bbu abunda xakiyi se idan ya amince, shashasha makwad'aiciyar abun duniya."

Nana tai murmushi tace "da kyau! Aaseey kinfi wannan shashashar k'awat taki ma d'aukan xafi bansan meyasa ba, ko da yake ba se na nemi dalili ba, dan banida lokacin ku, abun duniya da kikace ina kwadayi kuma xansamu very soon, ba abun duniyan kadai ba harda me abun duniyan wato mus'ab, ina tausaya miki jawahir a lokacin da mus'ab yadawo nawa, agabanki xan juyasa son raina."

Daga nan ta fice a d'akin, jawahir ta kalli Aaseey tace "kiyi hkr Aaseey, wannan abun yafaru ne adalilina, nice silar shiganki matsalar nan tunda ni na gayyaceki xuwa da wuri ashe tsautsayi ne yake jiranmu kimin afuwa." Ta fasheda kuka.

Aaseey tace banaso kina bani hkr duk wani abu da ya shafe ki ya shafeni jawahir, nifa amintacciya ta a duniyar nan ke ce, ke 1naji na jitsu da ita acikin k'awaye tun muna mkrnt, bansan meyasa ba ke kuma Nana ne a gabanki lkcn, ko dayake bakisan asalin kalarta ba a wannan lkcn shiyasa, da kuma rabon tsautsayi, inaso ki rike ni kamar ke, dukwani farinciki ko bakin ciki naki mu jure shi tare, kimin wannan alk'awarin."

Jawahir tace "bbu abunda xaki nema kirasa a guna Aaseey kinmin hallaccin ryw gaba 1damn hk ko ke kike so nayi miki alk'awari, Nana kuma ki dauki k'awancenmu amatsayin k'addara dakuma rabon wahala, nagode da k'aunar da kike mini Aaseey."

♥♥♥♥

Polisawa bincike suke lyk no other kamar ansace 'yar shugaban k'asa sbd yadda mus'ab ya d'aga hnkln sa akan lamarin.

Kowa yana cikin tashin hnkl har kwana3 batareda jin lbrn komi ba kuma har yau layin Nana baya shiga, gidan Su kuma anje yafia irga kullum a rufe da babban kwad'o.🔒

Aaseey da jawahir suna cikin wahala a kwanakin nan dan sau 1suke samun abinci a rana, ga xafin tsiya a d'akin, tabbas Nana ta cika marar imani.

Aaseey bata tina da twins dinta ba se da dare yayi kawai suka fad'o mata, lkcn kusan ten, ta xanura jawahir tace "Aaseey menene?"

Aaseey cikin tashin hnkl tace "my Twins, na barsu a moto a k'ofan gidanki"
Jawahir tasa salati tace "yanxu ya xamuyi? Allah kasa basuga yaran nan ba".

Dukansu hklnsu yatashi se a lokacin Aaseey ta tino wayarta dake aljihun jeans d'inta, ta kalli Jawahir tace "wayana yana aljihu bari na kira dadday'nsu."

Jawahir tace "alhmdllh amma ya za'ayi wayan tafito har ki kira tunda hanunki a d'aure ne?"

Aaseey ta sauk'e ajiyar xuciya tace "bamuda mafita shikenan twins d'ina."
Jawahir tace "kibar fadin hk Aaseey kiyi fatan alheri Insha'allahu suna cikin kulawar ubangiji."

A haka suka dangana dan basuda solution.

_*Sajna ce!*_
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*176↗180*

Al'amarin Nana se a hnkl, ko sallah bata barin bayin allah'n nan suyi, koda yake itama batasan darajar sallar na bare na wasu ya dame ta.

Aaseey ta kalli jawahir tace "sister ya xanyi ne wayarnan ta fito? Ko xanyi ta tsalle neh?"

Jawahir tace "Idan kikayi tsalle ya fad'o kuma xe iya samun matsalar da baxayyi mana amfani ba."

Aaseey tace "toh har yaushe ne muna tare da waya bamuda yadda xamuyi."

Jawahir tace "ki bari xuwa da safe mu sake rok'onta ta sunce ke muyi sallah idan ta yadda ta sunce mu se mu cire wayan koh?"

Aaseey tace "idan bata yadda ba kuma pha? Kinsan kowani lokacin sallah haka muke fama da ita."

Jawahir tace "mudai gwada, ni ina tunanin kada wayar tasamu matsala nw taxo bata

amfanemu ba kuma kinsan munada tsananin buk'atar wayar ko sbd muji labarin twins ma."

Aaseey tace "toh allah ya samar mana mafita."

*Amin amin na fad'a nida members na dandalin sajna.*

Washe gari bbu irin rok'on da basuyi ba tace baxata sunce su ba, haka suka hakura seda ta kawo musu abinci one plate kmr kullu sanna ta sunce musu hannu tace "ten minutes na baku kugama in d'aureku."

yunwar da sukeji ba kad'an bane ga abincin d'an d'is a k'asan plate, bbu yadda suka iya dole Aaseey ta hak'ura ta barwa Jawahir abincin, se da sukayi ta jayayya sannan jawahir ta yadda xataci abincin ita 1. Nan ma se da Aaseey ta nuna mata illolin xamanta da yunwa a matsayinta na me juna biyu.

Nana kywa tan fita taje ta mik'e kan doguwar kujera a falon bata aune ba bacci ya kwasheta.

Kwanciya Aaseey tayi cikeda tausayin twins dinta tana rusa kuka, jawahir se rarrashinta takeyi se da tayi me isarta sannan ta bari, kamar wasa jawahir tace Aaseey tashi muyi alwalla kafun tadawo musamu murage sallolin dake kanmu, ta mik'e kenan se ga wayarta ya fad'o.

Ta kalli jawahir jawahir ta kalleta, da sauri Aaseey ta jawo phone in taga wayar akashe, jawahir tace "kunna mugani, allah yasa dai ba matsala ta samu ba."

Amin Aaseey ta fad'a ta kunna wayar da saurinta lafiyanta lau se dai akwai k'arancin chaji."

Jawahir tace "Aaseey ya bbu chaji sosai?"
Aaseey tace "kin san a moto nasa chaji se little mami ta fara jan phone in se na cire kawai nasa a aljihuna da nufin idan naje gidanki xan jona."

Aaseey tace "kira daddy'n su muji."

Kafun ta kira cikin Jawahir yayi wani irin juyi, tasaki wani wawan ihu tana kiran hasbunallahu, tana cewa "ki taimakeni Aaseey, xan mutu inbar duniya, Aaseey ki taimakeni cikina xan mutu"

Aaseey hnkln ta gaba1 ya tashi bbu abunda take illa xuvawa jawahir addu'o'i, cikin yad'an lafa ta kwanta ta rufe idanunta kamar me jin bacci se dai har ynx hanunta rik'eda cikinta sbd axabar ciwon da take ji.

kafun Aaseey ta kira kowa se ga message d'in mijinta ya shigo kmr haka.

*aslm my Aaseey, dan Allah daga kin  kunna wayarki ki sanar dani.*

*ku kwantar da hnklnku Allah yana gaba da Nana, very soon xaku fita daga kaidinta, ku mik'awa allah komai sannan Ki kula da cin abincin Jawahir kada ta xauna da yunwa sbd abunda ke cikinta, ki kwantar da hnkln ki twins kuma Hanifa da Nabila sun d'aukesu suna gun mummy'nki a yanxu.*

Wani ajiyar xuciya tayi lkcn da tagama karantawa, a xahiri ta furta alhmdllh.

Batayi wata wata ba ta danna masa kira, ringing 1 ya katse wayar ya kirata, bbu wata gaisuwa yace "my Aaseey wai ina ta kaiku neh?"

Aaseey kamar tayi kuka tace "ni ma bansan wajen ba, amma naji Jawahir tace OLD GRA ne tsohon gidansu Nana, wanda tun muna nursery suka bar gidan, ni yanxu abunda ya dame ni ma shine jawahir a kwance take bangane ma jikinta ba cikinta se ciwo yakeyi, kuka takeyi sosai har na tsorita dan Allah kuxo da wuri ku kaita asibiti."

Mijin Aaseey yace "toh ki turomin address d'in yanxu."

Tace "toh."

Ta katse wayar ta fara typing masa address d'in gidan.

Bbu jimawa ta tura masa, text d'in yana shigowa yayi wa mus'ab da police forwading message d'in.

Lokachi 1 mus'ab ya kira police sukayi mgn, ya kira papa ya sanar.dashi sannan papa yaturo big bross suka had'u da mus'ab da police d'in, suka bi office d'in mijin Aaseey suka had'u suka tafi.

Moto biyar, d'aya mus'ab da mijin Aaseey, d'aya big bross, uku kuma na polisawa.

Dukansu gudu suke shararawa ba wasa har suka iso wajen.

A haka suka iso old GRA gidan da aka tsare su jawahir da Aaseey.

Polisawan ne suka xagaye gidan gaba1, mijin Aaseey ya kira wayar Aaseey, tana amsawa ta fashe masa da kuka tana cewa "Jawahir ta suma wlhy bansan ya xanyi ba, ina tsoron kada Aaseey ta tafi ta barni dan Allah ku taimaka kuxo ku.kaita.asibiti a dubata."

Mijin Aaseey ma hnklnsa ya tashi yace "subhanallah, yanxu ina Nanan take?"

Cikin kuka Aaseey tace "Tan falo na lek'a naga tana bacci".

Yace "Toh ku kuma kuna ina?"

"Muna wani room a sama naga an rubuta room3 asamn d'akin."

Yace "toh gamunan a k'ofar gida, amma ki nitsu muna tare da polisawa neh."

kaitsaye suka shiga gidan, Nana suka tarar a falo.tanata sharar bacci, ga kwalban giyar whisky a kusada ita da tutolin wanda seda taga bayansu sannan ta kwanta.

Polisawa ne suka tsaya akanta, da sauri su mus'ab suka hau neman Room3. Suna hangoshi suka d'uru ciki.

A kwance jawahir take cikin mawuyacin hali har yanxu hata farfad'o ba.

Aaseey kuma rik'e take da kan jawahir a kan cinyarta tana yi mata addu'o'i.

Bbu wata wata mus'ab ya sungume ta se motonsa, Aaseey ma suka fito tareda me gidanta da big bross.

'Yan sanda kuwa suka tashi Nana, wata 'yar sanda mata biyu ne suka cakamo kwalarta suka sanyata a moto.

Aaseey tashiga moton da aka saka jawahir, mus'avb ne yake jan moton, big bross da mijin Aaseey ne suka shiga moton big bross, polisawa kuma suna moton su tareda Nana.

Direct station suka tafi da ita, su jawahir kuma se asibiti.

_*Sajna ce!*_
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*181↗185*

Kai tsaye emergency aka wuce da jawahir, Aaseey ma ganin yadda ta xabge seda suka sa mata k'arin ruwa.

Sun tabbatar da cewar k'waya akasa cikin abinci na xubarda ciki. Kuma cikin Jawahir yafi watannin abortion, shiyasa be xube ba amma tabbas k'wayar ya tab'a d'an dake cikin domin k'wayar tanada k'arfi.

Kuma se anyi mata tiyata an cire yaron sbd gudun kada k'wayar ta kashesa aciki kafun ranar haihuwarsa.

Jawahir batasan halin da take ciki ba, Aaseey kuwa kuka da kuka, Haka mus'ab da sahib sukai signing aka yi mata aikin.

an fitoda yaro kam sede jikinsa ya kwakkwaile, abun ya tab'a fatarsa neh, yaro kam kyakkyawa dashi bouncing baby kmr ba jinjiri ba sede nana ta cucesa.

Labari ne ya iso musu cewar an d'auke nana daga station d'in ma'ana anxo angudu da ita cikin dare.

Bbu wanda beji bak'in ciki ba, babu kmr dr.shahid daya dawo k'asar a ranar.

HnkInsa yagama tashi ganin yadda jawahir da Aaseey suke rame suka kod'e. Duk da cewar shi d'in ma ba k'aramin sauyawa yayiba, duk damuwar rashin jawahir ta maida shi wani iri kmr ba kyakkyawan dr da muka sani ba. (Allah sarki rashin masoyi ba dad'i).

Da shi akayita hidimar kulawa da marassa lafiyan. Shi ya nemi aka maida kulawar jinjirin asibitinsa sbd dAma ba Jawahir ke shayar dashi ba, suna bashi madarar dake k'ara wa yara kuxari ne wato NAN.

Tun ranar bakwai sukayi masa rad'in suna da Shahid.

Dad'i kashe Doctor besan ma me xaice musu ba sbd farinciki.

Wata uku kacal ya d'auka yaro yakoma fresh, fatarsa kmr anyi masa sabo. Jawahir taji dadi sosai ganin yadda yaronta yayi kyau.

Bayan watanni uku again. Jawahir ma ta gama yin sauk'i, duk wannan watannin nan kuwa a asibiti tayi su.

Seda ta koma gida sannan akayi bikin suna lyk no other, akwati 4 mus'ab yai mata na suna

tareda key'n moto da gida.

Jinjiri little dr ma akwatunansa 3 babansa yayi masa na kayan suna da gida.

Dr ma key'n moto da gida yabawa jawahir, yayi wa yaro kuma akwatuna 3,na me suna, amma jawahir tace abun yayi yawa, seda suka kai ruwa rana sannan ta karb'a tareda godiya.

Aaseey ma ba'a barta a baya ba, akwati biyu tayi 1 na yaro 1na mamar yaro.
.
Ansha bidiri da kud'i sosai kmr ba neman su akeba.

Bayan ta koma gidan mami da 2 week se ga su mus'ab, sukq gaggaisa akayi tad'i kmr kullum daya tashi tfy se yace yanason mgn da yaya sahib.

Ba wani jimawa sukayi ba, yaya sahib ya dawo se ya kira Mami gefe sukayita mgn.

Naga dai jikin mami yayi sanyi, se kuma naji tana cewa "Allah ya zab'ar mana alherinsa kawai."

Bayan kwana biyu se gani nayi ana d'an hidimomi a gidan mami, Aaseey kusan kullum tana tare da mami suna k'usk'us.

Kawai rannan mami ta kira Jawahir d'aki ta gama yi mata nasihun duniya, ta gama nuna mata komai ya samu mutum k'addararsa ce hkn sannan ta furta mata wani mgn wanda nakasa fayyace Jawahir farinciki tayi da jin mgnr ko bak'in ciki.

Ba wani mgn ta furta ba face "Jawahir ki nitsu kiji abunda xanfad'a miki a yanxu ke ba matar mus'ab bace ke matar dr shahid ne, banaso kiminn hargitsin dakikamin a aurenki da mus'ab, sbd kowa yasani dr xab'in ranki ne, mus'ab dinma bawai kin k'isa bane, amma kowa ya sheda kinfison dr kuma sonda kike wa mus'ab bekai 1 cikin biyun na dr ba, shiyasa mijinki mus'ab dayaxo da shawarar nan bbu wanda ya hanasa, sbd shima dr yayi masa halacci a baya, shima kuma yaduba halin da dr yake ciki na rashinki ya tausaya masa ya sadaukar masa da ke amatsayin kixamo matarsa ta sunnah.".

Jawahir dai kanta yad'au chaji da alamun itama batasan farinciki takeyi ko bak'in ciki ba.

Tana jin mami tacigaba da cewa "Dr mutum.ne me halin k'warai ya cancanci fiyeda haka ma in akwai dama,, kuma yacancanci a tausaya masa a shekarun da yake ciki ace bashida matar aure. Kuma duk sbd ke yace baxai auri kowa ba".

Jawahir cikin sanyin murya tace "mami zuhra fa?"

Mami tace "wai ya rabu da ita tun bayan aurenki da kad'an lokacin da ta zubda cikinta tashe shiya bata maganin zubarwan kafun yayi tfy, wannan shine silar rabuwarsu."

Jawahir tace "mami a inah kukaji hkn?"

Mami tace "Shi ya fad'a.min ai muna waya da Shahid tun da ya tafi, baya sati be kirani ba, kece de kawai bakwa waya dashi amma Aaseey ka yana kiranta."

Jawahir tayi shiru tana juya mgnr a ranta.

Mami tace "Jawahir ki nitsu ki kula da aurenki, daga wannan auren bana kiki fatan asake wani dawo dawon, kuma kada ki d'aga hnkln ki da mus'ab Allah ze sa masa sassauchi ko dan tausayin dan uwansa musulmi da yayi, Allah xe bashi ta gari, kina ji na?".

Tace "Eh mami insha'Allah xan kiyaye."

"Yauwa autana d'iyar arzik'i, Allah yaimiki albarka ya baku xaman lafiya."

Tace "amin, amma mami kenan mus'ab sakinq yayi?",

Mami tace "Autana ai bawai ya sakeki sbd bayason ki ba ne, dalili ne ya sanya hkn, ki rok'i alah alkairinsa a rywrki kinji."

"Toh mami insha'Allah."

"Yauwa Allah yayi miki albarka, naji Aaseey tace tanaso ku had'u yau, anjima seki shirya kije gidanta."

"Toh mami."

Yamma nayi ta shirya se gidan Aaseey tana shiga tasamu twins a tsakar gida suna wasa da teddy, ta tallafosu tana basu sweet.

Aaseey ta fito tana cewa "amaryar doctor, shiyasa naji gidana yad'au warin asibiti, ashe matar likita ne ta bayyano."

Jawahir tace "hmm Aaseey knan."

Aaseey tayi dry tace "sunche mini little doctor'n mana, kin d'orashi abaya yadda ake xafin nan."

Ta sunche sa tana cewa "gashi nan kyaji da tsokanarki ba amsa miki xanyi ba."

Aaseey tai dariya tace "toh ki k'ariso ciki tunda ba amsa mini xakiyi ba matar likta hala yau sarautar ne.ta motso."

Jawahir tashiga falota xauna takalli Aaseey tace "wai meyene kike ta had'ani da likita kam?"

Aaseey tai dariya tace "oho, sw next week xakiyi bayani."

Jawahir tace "meyene a next week in?"

Aaseey tace "xadai kigane, se mun rufaki mun kaiki inkika fara kukanki na shagwab'a ko waiwaye baxamuyi ba."

Jawahir tace "baki da dama, nikam.kibani abunda xansha, idan kuma k'aida xakiyi min yaukuma se.muji."

Aaseey ta mik'e ta d'auko mata drinks ta ajiye tana cewa "na isa inyi miki k'a'ida ne? In nayi ma nayiwa kaina, ai dole inbi amaryar likita a sannu ko dan d'an xaxxab'in da nake d'an ji ajikina."

Jawahir tace "xaXxab'i.kike a hkn?"
Aaseey tace "hmm xaxxabin se safiya da yamma sosai yake xuwa."

Jawahir tace "wow, barka."

Aaseey ta d'aka mata duka tace "meye barka kuma? Lalle ma inace miki banida.Ify kina yin barka, keda mami bari na d'auko phone ina "

Jawahir tace "barka mana me sunana xataxo duniya."

Aaseey ta xaro.idanu tace "a ina?". Jawahir tanuna cikinta tace "anan."

Aaseey tace "rufamin asiri mana ke kuma, ko ciki ma nakeda shi wa yace miki xanyi miki me suna? Tabd'ijam.kalan ma tayi halin ki in kaita gidan miji tayita misbehaving?"

Jawahir tace "au haka kikace.? Toh kiran me kikayi min?".

Aaseey tace "mgnr hidimar biki ne nace kixo muyi shawari da events in da xa'ayi."

Jawahir tai ajiyar xuciya tace "meye labarin mus'ab?"

Aaseey tace "Normal, yana lafiya mana, jawahir kada ki d'aga hankalinki akan mus'ab fa,

saboda kowa yasan kinfi son dr a yanxu, mus'ab kuma da kansa ya yanke shawarar sadaukarwa dr ke, kuma cikin ikon Allah yana iya kokarin sa wajen kore dukkan wani tunani daxai daga masa hankali, abunda yadace kawai shine kiyita masa fatan alheri, muyita addu'a Allah yabashi ta gari kamar ke. kinji?"

Jawahir tace "amin", tayi murmushi sannan tace "amma ai dazu kince niba ta gari bane tunda ina misbehaving da aka min aure."

Dukansu sukayi dariya sannan Aaseey tace "muyi maganar biki, doctor sunxo tareda sajida dazu tashigo da memo wai muyi list din abunda ake bukata dakuma events din da za'ayi, yana jiranta a waje, se nace tabari in kinxo munyi shawara se in kirata."

Jawahir tace "bikin naki ne ai, kece da komai, ni de abu 1xan fad'a k'ara'in da ba'aimin a auren fari ba se an biyani a wannan, dan baxan yadda kusake min traditional wedding ba"

Dukansu sukai dariya Aaseey takawo mata pizza, ita kuma ta koma gege tana rubuta duk wani abunda ya kamata ayi a hidimar bikin.

Dare nayi Yaya Saahib yaxo ya d'auketa a moton sa da ya saya last month.

*Few days later.*

Duk wani shirye shirye na bikin jawahir da doctor ya kankama, ranar tarewa ake jira kawai domin an riga an d'aura aure.

Aaseey kuwa ga biki n aminiya ya taho se dai jiki ba k'wari, kullum cikin laulayi take, yau fari gobe tsumma.

Jawahir kuwa tsiya take mata son ranta, ita a dole xa'a haifa mata me suna.

*sajna ce.*
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*186↗190*

Aaseey har ledar ruwa aka d'aura mata sbd yadda ta zabge, duk zazzab'in nan ya jemar da ita kamar ba Aaseey white da muka sani ba.

Hakan yasa jawahir da doctor d'aga hidimar tarewarsu se aminiyarsu ta samu lafiya, jawahir ne takoma gidan Aaseey tAna kula da ita ta hutar da mummy'n Aaseey, lalle mummy taji dadin hkn sosai tace "kai wannan aminta naku yayi k'arfi jawahir, Allah ya sanya muku albarka da rahmatsa a rayuwarku gaskiya kin kyauta nagode sosai."

Jawahir tace "amin mummy ai Aaseey tafimun duk wata k'awar duniya, hasaluma ni a yanxu banida wata k'awa ta jikina irin Aaseey se kuma sajida, kinga kuwa Aaseey ta cancanci fiyeda haka ma a guna musanman idan na duba irin halarcin tayi ta min a rayuwa a lokuta mabanbanta, da irin wahalar datasha agun Nana sanadina amma duk da haka ta nunawa duniya cewar tana tare dani, dole in godewa Allah daya bani Aaseey kuma inyi mata hidima da dukkan lokacina, dan haka mama kibar yin godiya akan duk wani tsakanina da Aaseey, sbd Aaseey tawace nima kuma ta Aaseey ne".

Mummy taji dadi tace "toh Allah ya k'ara albarka jawahir yak'ara muku dankon aminci."

"Amin mummy kije gida kihuta, i will take care of everything insha'Allah".

Mummy tace "toh shikenan, amma teins fa? Kinga nanny'n su bata nan, ko xan tafi dasu, kada wahalar tayi miki yawa."

Tace "mummy aikin Aaseey ba wahala bane awajena, haka yaranta ai yarana ne, kibarsu kawai inkin tafi dasu ma kayya-kayyansu ne xai hanaki baccin rana, kinsan yanxu basa zama waje 1."

Mummy tace "toh shikenan, amma akwai wata sister'n Aaseey 'yar k'anwata taxo garin nan a week.innan xan turota se ta ringa tayaki d'awainiyar yaran".

Jawahir tace "toh mummy mungode."

Sukayi bankwana.mummy ta tafi.

Aaseey ta damk'e hanun jawahir tace "Nagode sosai da k'aunar da kikemin jawahir, nima banida kamarki acikin k'awaye, nagode sosai *matar likita."*

Jawahir ta lakace hancin Aaseey tace "bakida lafiyan ma se kinyi tsokana koh? In kika saje yimin godiya xan had'aki da maminki, kuma ni ba matar likita bace ni likitar ne gaba1, kuma kin lakatowa kanki dan yau xakiga aikin likitoci, se na tabbatar miki cewe me suna na tana hanyar xuwa duniya".

Aaseey tace "ni fa ba ciki ne da ni ba kawai zazzab'i ne  na zafi, amma ni ban d'au komai ba, kwata kwata ma twins shekarunsu biyu ne fa."

Jawahir dai batace komai ba ta yiwa doctor shahid waya.

"Hello doctor ka aiko mana sajida ta pt mana."

Yai murmushi yace "ok, ta yadda xata gwadane?"

Jawahir tace "ai ko dolenta, tunda an fad'a mata tak'i yadda."

Yace "toh insha'Allah xata kawo muku anjima."

"Toh bye, mungode."
"Ba i love yhu?" Ya tmby cikin tsokana.

Tace "Toh, i love yhu my Man."
Yace "gud, i love yhu too my princess."

Tayi hanging tana dariya.

Aaseey tace "jinya kikemin ko soyayya?"

Jawahir tace "duka nake had'awa sbd jinyar taki ta masoyin ne, abunda yashafi asibiyi kinga se an had'a da dr. Musamman ciki me tsada irin wannan."

Tayi pointing cikin Aaseey, Aaseey ta doke hanunta tace "banason iskanci wlhy."

Dukansu sukayi dariya, Aaseey tace "wlhy kwad'ayin awara nakeyi"

Jawahir tace "kinji ai, bari nayi sauri nasamo miki abakin titi kada me sunana taji haushina."

Ta d'au kud'i a purse ta fita, tana cewa "na nawa kikeso?"

"Na 500".

Jawahir ta juyo tace "kee! Wai me kika xama neh? Guda hamsin ne fa d'ari biyar."

Aaseey tace "da gaske xan iya cinyewa dan banason cin abincin rana yau, kema seki sayo naki dan ba zan tsam miki ba."

Jawahir dai ta fice agidan, a bakin gate tayi karo da wata kyakkyawar budurwa fara sanye da doguwar rigar atampa da gyale lemon green, tayiwa jawahir murmushi tace "Adda jawahir koh?"

Jawahir tayi murmushi se de cike takeda mamaki tace "eh jawahir ne."

Yarinyar tai murmushi tace "sunana meenal, ni 'yar umman Aaseey ne daga Abuja, mummy ne ta aikoni na tayaki ayyuka, naga kinyi mamakin yadda na sanki koh, toh nasanki ne a photo adda Aaseey tanunamin ke, tacemin kece best friend inta kuma u're good."

Jawahir tayi murmushi tace "sistee meenal kin burgeni sosai, yanxu abunda xa'ayi shune kixo ki rakani bakin hanya ku sayawa Aaseey awara."

Meenal tace "toh muje."

Suka d'au hanya se tad'i sukeyi kamar sun saba."

Lokaci 1 jawahir taji son meenal yashiga ranta kamar yar uwarta ta jini."

Haka sukaje suka dawo, kuma sukaci gaba da gudanar da al'amuransu acikin gidan cikin k'aunar juna kowa.yana mutunta d'an uwansa.

Gwaji da akayi kyma ya tabbatar Aaseey na d'aukeda cikin wata biyu, kowa murna yakeyi da wannan lamarin.

Da yamma lis yaya saahib ya kawo mami taxo sake duba jikin Aaseey.

Suka gaggaisa aka hau tad'i dan yanxu ita kanta Aaseey'n ma ta warware sae dae abunda baza'a rasa ba.

Meenal dake d'aki tana kwalliya ta fito sanye da doguwar rigan kanti dark blue, tasha kyau sosai kasancewarta fara sosai kykakkyawa kamar Aaseey."

Ganin mutane da yawa a falon yasa tayi saurin komawa d'akin ta d'auko mayafin rigar shima dark blue ta yafa akanta ta fito.

Har k'asa ta zauna sannan ta gaida mami ta gaida ya saahib cikin mutuntawa, Aaseey tace "meenal wannan itace mamin mu se yaya sahib babban yaya."

Meenal tace "ayyah sannunku da zuwa mami, yau Allah yasa naganku."

Mami tace "sannu yanmata," ta juya ta kalli Aaseey tace "Ina kuka samo wannan kuma, duk da nasan 'yar uwarki ne saboda kuna kama amma tayi min kama da 'ya'yan larabawa sbd har tanaso ta fiki kyau da haske."

Meenal ta rufe fuskarta da mayafi tana murmushi sbd kunyar mgnr mami.

Aaseey tace "yar ummana ne daga Abuja, sunanta meenal."

Mami tace "meenal sannunki da xuwa, ya mutan gida?"

Tace "Ify lau."

Jawahir kuwa idonta na kan ya sahib wanda duk hankalinsa ya koma kan meenal tun fitowarta, ko kyafta ido baya yi sbd yadda yarinyar ta burgesa.

Jawahir ne ta d'an tab'osa se a lokacin yadawo hayyacinsa, ta d'aga masa gira alamar tmby, kawai ya saki wani murmushi ya kanne mata idanu .😉

Tayi murmushi ta kauda kai.

Da dare jawahir da Aaseey suna xaune tareda meenal dake yiwa twins kwalliya.
Jawahir tace "meenal mijinki xaiga kwalliya kam, dubi fa yafda kiketa hadar da yarannan."

Tayi dariya tace "Adda jawahir kenan, ai kwalliya shine mace, nikuma haka kawai nakeson kwalliya."

Aaseey tace "kwalliya ba.miji asaran powder ba."

Meenal tace "Adda Aaseey kinamin tsiya son ranki kinsani dae mijinki ma ya fad'a nafiki kyau dan haka kinga mijin ba wai na rasa bane kawai dai ina abunda yake gabana ne tukunna kafun a iso kan mazan."

Jawahir tace "kwantaR da hankalinki sister meenal inma asaran foundation ne dai kin fita kyau a haka nesa ba kusa ba, kuma itama tasan hakan."

Meenal tace "yauwa Adda Jawahir, lokacin da xan fidda miji ai ita kanta setaga banbanci da lokacin nasu soyayyar."

Jawahir tace "fad'a mata kam."

Aaseey tace "au abun na yan ubanci neh?"

Jawahir tace "fiye ma da haka ai, ko ba komai ina bayan meenal bare kuma...."

Aaseey tace "bare kuma meye? k'arisa mana."

Meenal tace "bare kuma akwai komai, na k'arisa mata."

Aaseey tace "toh meye ne komai d'in?"

Jawahir tace "no ur water inside, wannan tsakanin mu ne."

Itadai meenal batasan inda jawahir ta dosa ba kawai tana biyewa jawahir din ne sbd su shak'ar da Aaseey, yayinda jawahir kuma akwai inda maganar nata ta dosa.

Washe gari jawahir ta koma gidan maminta tabar Aaseey da meenal.

Meenal kam bataso ba sbd sun sjaku da jawahir, haka ta saba yiwa shahid (little doctor) wasa, dan tanada son yara.

An gama seta ranar tarewa sbd Aaseey tagama yin sauk'i.

Yaya sahib kuwa ya gama fad'awa kogin son meenal, ji yake duk duniya bbu kamarta a mataye, Shiyasa yanxu yadau duk wani girma ya bawa su Aaseey da Jawahir sbd su tayasa campaign.

Anyi kamu a bikin sannan akayi walima, se ran lahadi akayi dinner, komai cikin tsari da wayewa akayi, 'yar wak'a aka sanya na nura m inuwa *Na fad'a miki sirrikan raina gaskiyar zance ina sonki.*se da gurin yayi shiru sannan mc ya kira amarya da ango tareda babban aboki da babbar k'awa.

Bbu jimawa doctor kabir da Aaseey suka fito filin, amarya da ango kuwa har da jawa mutane rai tukunna, kafun su fara takowa tsakiyar filin rik'e da hannun juna, sanye take cikin wata had'add'iyar wedding gown sky blue da head dark blue, tasha makeup sosai, shima sky blue jompa ne a jikinsa me aikin dark blue, sungama yin kyau karshe, suna idowa tsakiyar filin aka sake musu wak'ar m inuwa me taken *Amarya 'yar amana.*

A hankali suka d'an taka rawa sbd dukansu basuda rawar kai sosai, a nitse akayi hotuna aka gama komai aka watse.

Da dare kuwa aka kai amarya gidan mijinta dr shahid.

Daganan biki ya watse.kowa yana musu fatan alheri.

*Sajna ce!*
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*191↗195*

Se kusan ten sannan doctor yashigo gidan, har yanxu tana kudundune cikin mayafi akan gadon.

Da sallama ya shigo a hankali ta amsa tareda sake sunkuyar da kai k'asa.

Ya k'ariso tareda aje ledojin hanunsa, yace "matar likita."

Ta d'anyi murmushi a hankali tace "har da kai koh?"

Yace "nima nabi bakin aminiyarmu Aaseey neh."

Batace komai ba yace "ya hidimomin biki?"

"Lafiya lau alhmdllh" ta amsa a hankali.

Ya sake cewa "sannu da k'ok'ari nasan an wahal min dake ba kad'an ba."

Tace "uhm Aaseey ne tayi komai ba ni ba."

Yace "Ayyah Aaseey'n nan tana sonmu da yawa."

Tace "ba laifi, mu ma kuma muna sonta."

Yace "ina yaronmu little doctor?"

Jawahir tace "Aaseey ta k'wace mana yaron mu wai se bayan 3days."

Yace "A'a gaskia ban yadda ba, se dai a bamu yaronmu gobe, dan ni bazan iya jure rashin sa ba, ko ke zaki iya?"

Jawahir tace "nima banason yayi mana nisa amma tunda tace ya karba ba laifi itama mahaifiyarsa ce".

Doctor shahid yace "Hakane amma gaskia gobe zan karb'o mana yaronmu."

Kawai tai murmushi.

Yace "matar likita ki tashi kiyi alwalla muyi sallah mu godewa ubangiji daya nuna mana wannar ranar da muka dad'e muna jira, sannan kichi abinchi ki kwanta ki samu ki warware gajiyar biki".

Tace "toh likita."

Yai murmushi yace "sabon suna?"
Itama tace "Sabon suna?"

Dukansu sukayi dariya, sannan ta sauk'o, tashiga bathroom tayi alwalla tafito, sukayi sallar nafila raka'a 2 sannan yai ta jreo musu addu'o,i, dag bisani suka jawo ledar kaza, da kansa yake bata naman kazan har ta k'oshi sannan yaci shima.

Wanka tashiga yi, shima yawuce d'akinsa yai wanka sannan ya dawo.

Har ta kwanta se de ba bacci takeyi ba se aikin danna waya.

Yasa hanu ya karb'i phone d'in yace "matar likita ki temaki likita ki hutawa jikinki."

Tai murmushi tace "toh likta, naji, rufemin data se ka aje wayan."

Cikin murmushi yayi mata yadda tace sannan yace "angama matar likita."

Tai murmushi tace "toh ka tafi room in ka seda safe."

Yace "abun harda rowar d'akine? Toh na tafi tunda haka kike so, bye seda safenmu."
Ya manna mata kiss a goshi sannan yace " u're smelling good matar likita."

Tai murmushi tace "stoh nagode seda safe."

Ya fice tareda ja mata k'ofan d'akin. Ya nufi dakinsa ya kwanta, dukkaninnsu akwai hidimomi da gajiyan biki yasa bacci yayi awon gaba dasu da wurwuri.

Da asuba ya tashi yayi alwalla sannan ya tasheta, shikuma yatafi masallaci, yana dawowa ya shigo d'akinta, akan sallayar ya sameta tayi bacci, jingine da gado.

Ya cire mata burmemen hijabin da tasa sannan ya d'agata ya maida ita kan gado ya sanya mata pillow sannan ya d'auko wayarsa yafara d'aukar hoton kyakkyawar fuskarta.

Yakai hoto goma yai mata sannan ya dawo kusada ita ya kwanta tareda rungumeta a jikinsa.

Shima besan sabda bacci ya d'aukesa ba.

Har kusan ten sannan ta farka, ta juya ta kalleta rungume a jikin doctor'n ta, tayi wani murmushi taja karan hancinsa tace "my likita kenan."

Kai tsaye ta mik'e tashiga toilet tayi wanka sannan ta dawo jikin drawer ta fidda wani riga da skirt na atampa red colour, ta zauna tayi makeup d'an daidai.

Sannan ta nufi inda doctor yake ta zuba masa idanu, cikeda k'aunarsa, daga k'arshe ta dangwala masa kiss a kumatu wanda yai sanadin farkawarsa.

Da murmushi ya kalleta itama haka tayi masa, yace "Matar likita irin wannan kyau haka?" Tai murmushi tace "likita ka tashi kayi wanka kafun na had'a mana abun karyawa,"

Yace "wani abun karyawa kuma? Ai baki isa kice xakiyi girki ba a satinnan duka."

Tace "sbd meye?"
"Sbd likita yanason matarsa."

Ta noke kafada tace "matar likita kuma se tayiwa likita girki."

Yace "sbd meye matar likita xata wahal da kanta?"

Tace "sbd matar likita tanason likitan ta."

Yai murmushi yace "inhar matar likita da gaske tanason likita toh ya kamata ta huta ba yanxu ba tukunna."

Tace "shikenan tunda ka k'i."

Ya mikie ya shiga wanka.

Ba jimawa ya fito ta kawo masa wasu kanaban kayan da ta zab'ar masa a wadrobe d'insa. Wando jeans da red t-shirt, ta feshesu da turare se k'amshi sukeyi.

Bai b'ata lokaci ba ya kimtsa sannan taxo kusa dashi ta xauna tareda cewa "Ina kwana?"

Yai murmushi "Ify lau matar likita, ya gajiyar biki?"

"Lfy lau alhmdllh, ya naka gajiyan?"

"Nima Ify lau gajiya tabi Ify."

Tace "masha'Allah."
. yace "bari na kira sajida ta kawo mana abinchi koh?"

Murmushi.tayi ta gyad'a masa kai, yayi wa sajid waya.

Sannan yace "matar likita kixo kiyi kallo kafun ta iso.

Suka wuce parlour ya kunna musu kallo, tasar zeeAlwan.

Ba jimawa sajida ta shigo da sallama, jawahir ta tashi ta karb'a mata food flask d'in sannan ta rungumo ta.

Sajida tace "matar likita kinsha kyau pha."

Doctor shahid yace "ke! Bazaki ce aunty ba?"

Dukansu sukayi dariya tace "toh aunty jawahir matar likita."

Jawahir dai.binsu take da idanu yana murmushi.

Suka gaggaisa sannan suka hau d'an tad'i.

Jawahir tace "sis wai yaushe xamu kaiki neh kam?"

Tace "Ina?"

Jawahir tace "can d'in mana."

Dr shahid yace "ai wanda zata aura ya rasu kwanaki bayan tafiyata egypt, da tunin an kaita mun

huta"

Jawahir tace "ayyah sorry sister ya mukaji da hakiri kuma?"

Sajida tai murmushi tace "alhmdllh."
"Toh allah ya ji k'anshi."
Sajida tCe "amin, bari na tafi."

Jawahir tace "haba dai, daga zuwa se tfy? Kamar wani waje xaki koma? Keda kike nan cikin gida?"

Sajida tace "a'a gara dai na tafi kada na takura ku."
.
Dr yace "ke har kin kai ki takuramu ne a tunaninki? Ai ba wanda ya isa ya takura likita da matar sa."

Tace "uhm.ni naga sabon salo a wajenku toh sae anjima."

Jawahir tace "toh k'awalli ki gaida mummy."

"Toh xataji.",ta fice.

Dr yace "k'anwa dai ba k'awalli ba, ai yanxu kinxamo aunty'n ta."

Jawahir tace "tunanin wani abu nakeyi doctor."

Yace "toh, muje.kicu abinchi tukunna se ki.fad'amin."

Suka wuce dining suka ci abinci sannan suka dawo parlour.

Ya kira Aaseey a waya yana cewa "k'awarmu xamu zo k'arb'an yaronmu pha?"

Tace "Ai ka makara dan mami tace "wlhy kada na baku shi se bayan 3days, kaga yau anyi 1 se ka juri lissafi."

Yace "hkne abun?"
Tace "kwarai ma kuwa."

Yace "shikenan tunda mami tace hk mun hkr."

Tace "dayafi kam, ina jawahir?"
Ya mika mata phone tayi sallama tace "gani nan ya gajiyar biki?"

Tace "Ify lau, ya amarci?"
Jawahir data fita tsiya tace "Ify lau, ina fatan kina kula da me sunana?"

Aaseey tace "Ohon miki."
"Toh allah ya raba Ify, se nazo karb'ar haihuwa nida doctor na.".

Tace "allah ya kare."
Tayo hanging duka sukayi dariya.

Sannan yace "me xaki fad'amin d'axu?"

Tai numfashi sannan tace "maganar mus'ab ce, nasan yanxu haka yana cikin mawuyacin kewa, why not ka bashi sajida ya aura idan bbu matsala?"

Yai shiru yana naxarin mgnr daga bisani yace "kin kawo shawara me kyau amma xan k'ara tunani akai kuma in binciki ra'ayinta, in munji normal se mukaiwa su daddy mgnr koh?"
.
Tai murmushi tace "toh nagode sosai."

Yace "nine da godiya princess."

_One week later._

❤❤❤❤❤
Nana se kai kawo take a tsakiyar parlour'n gidansu dake bauchi, sbd nan suka koma itada mum tun da aka gudo da ita daga station.

Zuciyarta tamkar ta huga sbd hotunan dake baje kan kujerar parlour'n.

Nikuwa nawa gulsin be barni ba se da na duba, hoton jawahir ne a ranar dinner tareda mijinta dr shahid, se d'ayan kuma itada Aaseey da d'anta shahid little doctor.

A fili ta furta cewar ko da kin rabu da mus'ab sw na tarwatsa miki farincikin rywrki, se na rabaki da wannan d'an sbd ni ce macen da na dace da haifawa mus'ab yaron da xai gajesa ba ke ba."

Waya tad'auka ta kira kawarya shamsy, tayi mata bayanin komai, shamsy tace "akwai wata dillalliyar 'yan aikatau dana sani zata iya temaka mana."

Nana tace "me kike jufi,"

Shamsy tace "dole kije a matsayin yar aiki nana in de kinaso kiga bayan yaron nan.".

Nana tace "inde xansamu kusanci dashi har in illatashi toh xan iya komai shamsy kiyi mata

mgn."

"Toh in munyi mgn xan kiraki."

*Ku biyoni dan jin yadda xata kasance tsakanin jawahir da Nana.*

*Sajna ce!*
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*196↗200*

_*Two weeks later.*_

Gidan dr ana zuba love ba k'arya, kulawa ake sosai da juna, kowa yana burin kyautata wa d'an uwansa.

xuwa yanxu shahid ya dawo hanunsu, kulawa na musamman suke masa, musanmman dr shahid dayake maitar son yara, yad'au son duniya ya d'aura akan me sunansa little dr.

Duk wani motsin sa se yace ina little dr'n sa, shiyasa ma Jawahir hata damuwa akan al'amuran yaron sosai sbd doctor ya xamo masa tamkar Nanny.

Nana na gani cikin shigen ma'aikatan gidan, se shara take a b'angarensu na ma'aikata.

Ni kaina seda xuciyata ta buga, sbd ina tsoron sharrin Nana ayanxu.

Ya sahib da meenal sun dedeta kansu, ta gamsu da soyayyarsa kwarai a xuciyarta, shiyasa murna kamar ta kashesa ya koma gida ysna sanar da mami.

"Mami dama na fad'a kiki insha'Allah ni xan xab'a miki surka me kunya itin jawahir d'inki gashi kuma nasamo wanda har ta fita kunya ma."

Mami tayi dariya tace "tunda kana sonta ai xakace haka."

Yace "da gaske dai mami, Allah she's gud."

Tace "na yadda, yabvas meenal nada halaye masu kyau sannan tanada cikekkiyar kunya, kuma nagode wa allah data zamo surkata.".

Yace "yauwa mamin mu, xanyiwa su baffah mgn se suje abuja koh?"

Tace "toh ba laifi."

Yace "tnx yhu so much mami."

Tai murmushi kawai tace "may god bless yhu son."

Yace "ameen."

_*5months later.*_

Nana ta gama dukkan k'ok'arinta bata samu aiki a b'angarensu jawahir ba, tana aiki ne a quarters d'insu na yan aiki.

Hakan be yi mata dad'i ba, tagama duk yadda xata nemi shiga side d'insu ta rasa sbd akwai tsaro matuk'a.

Har ta kusan sarewa wata xuciyar tace "kidai k:ara hkr, ko xaki dace."

Kwance jawahir take kan doguwar kujerA tana kallo, sajida ta shigo da sallama tana cewa "Ki kawo little doctor ga babansa yaxo."

Jawahir tace "kije ki d'aukosa a room d'in doctor."

Tace "ok" ta shiga ta samesu a xaune doctor yana ta yi masa wasa, ga motoci a gabansa barkatai na wasan yara.

Tace "doctor  baban doctor."

Yace "ya son ranki?"
.tace "toh babansa ne yaxo."

Dr shahid yace "kice min daga gun hira kike mana."

Tace "hira kuma?" yace "au sorry, bari naxo, kije xamu taho dashi.".

Ta dawo parlour wajen jawahir tana cewa "Aunty wai wannan wani film ne haka?"

Jawahir tace "mijin biza."

Ta zauna da sauri tace "ah nasamu film.d'in da nake nema yau baxanje asibiti ba."

Dr shahid dake fitowa tareda shahid little dr, yace "baki isa ba."

Tai dariya tace "ji yayan nan dai, aikuwa da gaske nake xakasha kallo"

Yace "Shikenan" ya kalli jawahir yace "inaga itama xamu jonata da mijin bizan ne su k'arita can."

Jawahir tayi dariy tace "gaskiya kuwa da kinsha aure."

Tace "kwa ji dashi dai, kun shanya mutum awaje in baku manta ba." Ta cigaba da kallonta.

Dr yace "matar likita bari naje gun mus'ab a waje."

Tai murmushi tace "se kun dawo ku gaidashi."

Jingine yake jikin motonsa a k'ofar gate in gidan. Dr yai sallama sukayi musabaha sannan yace "ka shigo mana."

Suka shigo har cikin gidan, Ta k'ofar baya suka shiga k'aramin parlour'n bak'in.

Dr yayiwa sajida waya yace takawo musu abun sha, va jimawa takawo tareda cups akan tray.

Ta fice sannan suka sake gaisawa, dr yace "mus'ab ina ka shiga ne?"

Mus'ab yai murmushi yace "naje umrah ne."

Dr yace "tafiya bbu sallama haka? Kowa hnkln sa ya tashi?"

Mus'ab yai murmushi kawai ya sipping juice din sannan yace "ya d'awainiya da little dr kuma?"

Dr shahid yace "se kayi kuma ai, mutum da d'ansa se ance masa ya d'awainiya?"

Mus'ab yai murmushi yace "toh sannu da kokari allah ya biyaka da aljanna."

Ya amsa da "amin."

Shiru yad'an gudana a tsakani, sannan daga bisani dr shahid yace "mus'ab in tmbye ka mana?"

Yace "ina jinkq."
."ya batun aure?"

Mus'ab yai shiru kad'an sannan yace "bbu labari, har yanxu bansamu wacce naji xan iya ryw da ita ba."

Dr yai ajiyar xuciya yace "amma ya kamata ka k'ok'arta mus'ab, sannan abunda yasa na tmbye ka shine jawahir tayi maka zab'in matar aure tace in kanada ra'ayi."

Yace "wacece ita?"

Dr shahid yace "Sajidan mu ne."

Mus'ab yace "duk wani abu da yaxo daga b'angarenka kaida jawahir xan karb'esa hannu bibbiyu sbd muhimmancinku gareni, ina fatan allah ya sanya hkn ya xamto alkairi a garemu."

Dr shahid cikin farinciki yace "amin alhmdllh, naji dad'i sosai, ka kyauta."

Mus'ab yace "ba komai xannkoma gida."
Dr yace "haba dai tun yanxu? Ka bari kaci abinchi mana."

Suna cikin haka se ga sajida da tray d'in abinci, tayi sallama ta aje mus sannan ta juya.

Har taje bakin kofa dr ya kirata, ta juyo yace "zo ki zauna."

Ta dawo ta xauna tana binsa da idanu yace "ku gaisa bari naxo." Ya fice a d'akin

Itade mamaki takeyi su gaisa kuma na nawa kenan?

Mus'ab ne ya katse mata tunani da cewa "sannu da d'awainiya."

Ta yi murmushi tace "ba komai kai xa'ayiwa sannu da ziyara."

Yace "gud ya ayyuka?"

Tace "alhmdllh."

Yace "masha'Allah, kiyiwa dr magana xan wuce."

Tace "tun bakaci abincin ba?"
yace "na k'oshi yau, wataran xanci insha'Allah."

Tace "toh allah ya kaimu." Ta mike ta koma babban.parlourn.jawahir.

Tayi.sallama ta shiga tana cewa "yaya wai.kaje xe wuce gida."
Yace "tun.yanxu? Kodau kin kora mini aboki ne?"
.
Ta tab'e baki tace "nikuma meye nawa?"

Jawahir tace "zauna muyi kus kus."

Taxauna jawahir tace "har angama hiran ne?"
"Wai wani hira ne wannan kuke fad'a?"

Jawahir tace "shikrnan tunda baxaki bani labari ba, bari mijina ya dawo ya bani lbr."

Sajida tace "baku da matsala mutanen nan."
Jawahir tace "bamu dashi kam tunda kowa na tareda bugun zuciyarsa, kema kuma haka muke miki fata ki kasance tareda mus'ab d'inki."

Tace "mus'ab dina kuma?"
Jawahir tace "yes mana, ko bakyason baban shahid d'in nawa? Bakyaso shahid d'ina ya ce miki aunty? Ko kinfi so a auro wata wacce xata cutar mana dashi? Ki taimaka ki auri mus'ab ko dan d'ana shahid, ko dan halarcin da yayiwa d'an uwanki please."

Sajida tace "wannan dalilin ne yasa yaya ya tsaidani agun mus'ab? Amma ya zan auri wanda yake matsayin mijinki ada aunty jawahir?"

Tace "ada kikace ba yanxu ha, ni yanxu mijina dr ne, in har xuciyarki ta amince da mus'ab to oi karb'esa da xuciya d'aya kibar tunanin ma munyi wani alak'a dashi abaya."

A hankali sajida tace "Tohm aunty xan duba."

"Yauwa sister, har naji dad'i wlhy."

Se bayan kwana uku sannan sajida ta bada amsar amincewa auren mus'ab sbd ta riga ta rasa

masoyinta khamis.

Kowa yaji dad'in hkn kasancewar suna son farantawa mus'ab rai.

*Few months later.*

Mus'ab da sajida an manne, xuwa yanxu kowa yasaki jikinsa da juna, kuma mus'ab ya mance da kewar jawahir dake damunsa sede abun da baza'a rasa ba lokaci xuwa lokaci.

Sahib da meenal ma ansaka ranar engagement.

Labari.ya isowa Nana cewar mus'ab xai auri Sajida, xuciyarta ne kawai be buga ba amma ta kadu sosae.

Wasa wasa take shirya dukkan wasu plans inta tareda shamsy, kuma nan bada jimawa ba take shirin k'addamarwa.

*Sajna ce!*
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*201↗205*

Da sasafe akayiwa jawahir waya cewar Aaseey ta haifu, ba wani bata lokaci ta shirya ta tafi yayinda tabar doctor tareda shahid little doctor.

Kusan ten sannan dr ya fito shida shahid, kai tsaye dining ya nufa sbd yasan sajida xata kawo

masa abinci tunda jawahir batayi abun karyawa ba ta tafi.

Zama yayi yanacin abincin yana bawa shahid dake cinyarsa, wata daga cikin masu aiki (Nana ce, amma dr shahid besan ko wacecd ba sbd be tab'a ganin nana ba ko a hoto) tayi salama tareda durkusawa ta gaishesa.

Ya amsa a mutunce sannan yace "wani abun neh?"

Tace "dama...dai...naxo in d'auki shahid ne ..sbd naga mamarsa bata nan kaikuma ko xaka fita aiki."

Yace "toh ke a ina kikasan bata nan alhalin a b'angarenmu babu yan aiki?"

Ta sosa kai tace "Dama ai muna mutunci sosai da hajiyan kuma da xata fice mun had'u tace min xata unguwa kuma naga bbu yaron a hanunta, da na tmby se tace ta barshi a gida, nace mata idan ja gama ayyukana xan karb'esa sbd inason yaron sosai."

Dr shahid yai shiru sannan yace "Amman dai ni ba aiki xani ba yau, ina gida shiyasa ma ta barmin shi."

Ta mik'e tana cewa "toh shikenan, dama nayi tunanin ko xaka buk'aci hutu ne se in karb'a maka shi."

Har xata fita se dr yaga kamar in ya bari ta tafi ya gwaleta, yace "toh kixo ki d'aukesa, bari in shiga wanka,."

Tace "toh" ta k'ariso ta karbi shahid tana masa wasa "d'an mama da baba kasha wanka koh?"
Yace "ya sunanki?"
Tace "bojud'e ake kirana."
Yace "toh sannu bojud'e"

Dr ya bita da idanu yadda take wasa da yaron shikam ta burgesa yadda takeson shahid.d'insa amma ta bashi mamakin yadda ta dage xata kula dashi tunda mamarsa batanan, dan a iya saninta babu me xuwa d'aukar dr, dan kusan yafi xama tareda shahid d'inma fiyeda mamarsa, dan har asibiti.suna tafiya tare, yayi masa takeaway'n madarar NAN.

Kai tsaye wanka ya shiga, ita kuma bangarensu na yan aiki ta nufa ta shige dakinsu ta rufe.

Abincin ta na safe da bata ci ba ta d'auko ta ajiye, ta je ta bude wata drawer ta d'auko wani kwalba a farin leda.

Ta sunce ta bud'e kwalbar, ta jijjiga sannan ta tsiyaya abun kwalbar acikin abincin.

Ta maida kwalbar ta rufe tareda sawa cikin drawer ta.kulle, ta nemi takarda ta fara rubutu kamar haka.

*Dr shahid, ba dan kai na kashe yaron nan ba, na kashesa ne saboda jawahir mahaifiyarsa, kuma nayi hkn ne sbd a sanadinta ne mus'ab ya rabu dani, wannan shine k'aramin hukuncin da xan iya yi akansa, dan nayi alk'awarin nice ta farko da xan haifawa mus'ab d'an da xw gaji dukiyarsa, next target d'ina shine sajida.*

_*Naxo gidannn matsayi yar aiki ne sbd in cinma burina akan yaron nan, kuma yau burina ya cika, dan haka nasani Ikacin da kuka riski takardar nan nayi muku nisa, jawahir kinga sakamakon rabani da masoyina mus'ab.*_

_*Nana sunana ba b'ojud'e ba.*_

Ta ninke takardar ta ajiye kan katifarsu, ta sake ciro kwalban data ajiye d'axu ta bude tana sake tsiyayawa a abincin tana cewa "yau.xaka mutu dan ubanka, ka xage kana kallona.koh? Kai ga d'an gata? Kayi tunanin nima.bautar xanyi ta maka har uwarka ta dawo koh? Toh.ni salary'n gidanku.be damen ba, dan ba wani buk'atar kaina nake dashi ba, duk kud'in da.aka.biyan a gidan ubanka kai nakeyiwa sayayyar.wannan poison in, gashi kuma yau.ranar aikinsa yaxo shiyasa.na d'auki mafi tsadan domin inyi gaggaqan aika ka lahira."

Tasaki wani dariya tana cewa "sannu dan mama da baba, ci abinci koh?"

Ta tura masa plate in.gabansa.yasa hanu ya d'au spoon in, kunsan yarq da son cin abinci da spoon, yana ta k'ok'arin d'ebo indomie'n acikin spoon in taji ana doka.k'ofa.

Hankalinta ya gama tashi amma se.ta.dake.tace "waye?"

Dr.shahid yace "Baban shahid.ne, zan fitane na kawo miki. Madarar.sa sbd kada yayita kuka."

Ta.tura plate gefe ta boye.takardar a.k'asan.pillow ta bud'e.kofar.

Ransa amugun.b'ace yasa hanu ya d'auke shahid tareda k'wak'ulan bakinsa yaga ba komai alamar baici abincin ba, yace cikin tsawa"ina key.d'in dakin.nan?"

Jikinta na rawa.ta mik'a masa, yana fita ya.sawa.d'akin key.ta waje ya nufi sashensa.da key d'in.

Ashe y dad'e atsaye yana.jinta, dan haka Polisawa yayiwa waya ya sanar.dasu komai, bbu jimawa.suka ido sukayi awun gaba da Nana, tareda abincin, suka birkita d'akin suna neman

poison d'in, abinciken suka.gano takardar data rubuta.

Duka suka tattar.suka tafi dashi.
Shikuma ya rungume.shahid.ajikinsa yana cewa "Allah ka cigaba da karemin d'ana." Ya manna masa kiss a kumatu yacigaba da cewa "da na rasa ka da bansan irin tashin hankalin da xan shiga ba my son."

Jawahir kuma batasan anayi ba, tanacan gidan me jego data haifo namiji.

Sajida ma xata shigo gidan kenan taga yan sanda sunfita da yar aikin gidan.

Kai.tsaye part in Doctor tanufa tana tmbyrsa ya bayyana mata komai yakuma sanar mata cewar ashe Nana ce wannan d'in ba bojud'e sunanta ba.

Ta dafe k'irji tace "mun shiga uku, sharrin Nana har yakaiga kisa? Gaskia wannan lamari nata yana ban tsoro, Aunty Jawahir d'in bata dawo bane?"

"Eh se anyi azahar xata dawo tace."

"Toh Allah.yadawo.da ita Ify kuma ya kare gaba, amma yaya ya kamata kashe sbd kadasu k'ara gangancin bari a gudu da ita irin wancan karon."

Yace "dole na ai, ki rufe mana side inmu ki d'au shahid kutafi wajen mummy dashi, bari inje inmata bayani se in wuce station in."

Tace "Toh allah ya tsare."

Har yayi nisa ya juyo yace "kowace yar aiki ne tace miki xata rik'esa kada ki bata shi pa, ki lura dashi sosae."

Tace "Haba dai yaya, ai munga isharar yan aiki xuwa yanxu kam."

Ya wuce ya bawa mummy bayanin komai, ta jajanta masa tace "allah sarki, yaro beji ba be gani ba, yau inda hk ta faru ya uwarsa xatayi? Yarinya ta k'warai me tarbiyya?"

Doctor yace "allah ne kawai ya tsare."

Tace "Gaskia kam se a kula da gaba."

Yace "Insha'Allah."

Ya mik'e ya fita.

Kaitsaye station ya nufa, ya kuma tabbatar musu cewar dukkan shaida yanuna kashe yaron xatayi dan haka ba bailing, kotu xai shigar da ita.

Suma sun amince sbd ba yau aka fara kamata da laifi ba dan haka sun tsaida rana jibi jibi xa'akai Nana kotu.

Se bayan azahar Jawahir tadawo, taga b'angarensu a rufe ta wuce bangaren mummy.

Suna falo mummy na vawa shahid madarar sa, sajida kuma tana danna wayarta.

Ta shigo da sallama ta xauna, tayiwa mummy barka da gida sannan suka gaisa a mutunce.

Sajida tace "aunty sannu da dawowa"

"Yauwa sister" tabada amsa a tak'aice.

Mummy tace "ya kuka samu masu jegon?"
Tace "Ify lau alhmdllh suna gaidaku."

"Toh madalla, Allah ya raya mana."

Sajida tace "Aunty wai dawaye yaron yake kama?"

Jawahir tai murmushi tace "na d'auko miki hotonsa kafun kisamu xuwa, in kinga hoton xaki tantance."

Sukayi dariya mummy tace "kin tsareta da surutu ki bata key d'insu mana."

Sajida tace "auu, na mance ne yi hakuri aunty, muje in d'auko miki."

Ta d'auko key'n sannan mummy ta mata bayanin dayasa aka rufe wajen.

Ta xaro idanu ta dafe k'irji tace "innalillahi, nikam.na shigangad'i na da Nana, tabvas _*wata k'awar tafi guba*_ kuma na fahimci illar aminci da mutumin da besan halacci ba, tabbas nayi nadamar had'uwata dake Nana, amma ko ba komai kin k'ara mini ilimi cikin darussan rayuwa wanda xan koyarda mutane da yawa kuma in fad'a agaban.duniya cewar _*WATA K'AWAR TAFI GUBA."*_

Ta k'arisa maganar cikin kuka tareda rungume d'anta shahid tana shafa fuskarsa.

Tace "Allah ya cigava da karemin kai shahid"

Ta mik'e tana cewa "mummy barinje nayi wanka."

"Toh Jawahir kicire damuwar Nana a ranki kanar ma ba'ayi ba dan likita ya tabbatar cewa kaitsaye kotu xe makata."

Wasu hawaye suka gangarowa Jawahir tace "toh mummy nagode"

"Yauwa allah ya k'ara albarka".

Suka fice, sajida ne tayi rarrashinta suka gama ayyukan da xatayi na abincin dare, sukayi wanka, suka xauna kallo.

Kusan 5 Doctor yadawo, da saurinta ta rungumo shi tana cewa "u're welcm my Man"

Yai murmushi yace "matar likita me ya sakamin ke kuka?"

A hankali ta janye jikinta daga nasa tareda cewa "doctor?"

Ya kalleta yace "inajinki"

Wasu hawaye suka biyo fuskarta tace "Doctor wlhy  *wata k'awar tafi guba, wlhy Nana tafi guba yimin illa,*_ if not for yhu da shikenan ta kashemin shahid kuma ta kashe sajida sannan ta dawo kaina."

Ya rungumo ya ajiyeta kan kujera ya sgare mata hawayenta. A hnkl yace "data kashe *mana* shahid dai, point of correction, shahid namu ne ba naki ke 1 ba, kuma ki manta da Nana insha'Allahu jibi tana kotu."

Tace "nagode da yawa doc....."

Bata k'arisa ba ya rufe mata baki da hanunsa yace "shhh, kada ki sake yimin godiya".

Tai murmushi ta rungumw mijinta tanajin wani k'aunarsa a ranta.

Ya.d'ago fuskarta yai murmushi ya lakace mata hanci tareda cewa "me kuka da dariya"

Ta rufe idanunta da hanunta tace "yaushe xakaje ganin yaronmu?"

Yace "yau da dare insha'Allah keda sajida xaku rakani."

Tace "Allah ya kaimu, bari na kawoma abin sha."

Yace"ok" ta kawo masa juice da cup ta tsiyaya masa yasha sannan yace "maminmu tana gaisheki."

tace "ina amsawa kaje gidanta kenan?"
Yace "naje d'axu yimata barkan haihuwar yarta."
Tace "gskia kam, amma doxtor ya akayi aka d'au Nana aiki.agidannan baka sani ba?"

Yace " ai ba'a side dinmu suke aiki ba, b'angaren su mummy ne kuma mummy ne tA d'auketa dan duka gidannan bamusan itace Nana ba tunda bamu tab'a ganinta ba".

Ta gyad'a kai tace "allah ya tsare"
Sajida dake gefe tCe "yaya sannu da xuwa"

Yace"yauwa, yaushe kika shigo?"

Jawahir tace "muna tare pa tun d'axu."

Sajida tace "gani nayi daga welcm anshifa love shiyasa na barku."
Dukansu sukai Dai

da dare sukaje suka yiwa aaseey barkatu suka dawo, Aaseey tayi mamakin Nana kuma tace itama baxa'a barta abaya ba setaje kotu.

*Sajna ce.*
[6/1, 12:15 AM] Sajna: 🍀🍀🍀🍀🍀
*WATA K'AWAR TAFI*
*GUBA*
🍀🍀🍀🍀🍀

*TRUE LIFE STORY*

*••••••••✍ by Sajna.*

*206↗210*

Ranar Talata aka shigarda Nana kotu, Duk wani na kusa da Jawahir seda ya halarci kotun.

Bayan dukkanin shaidu da aka gabatar agaban kotun, alk'ali ya tabbatar da zargin da akeyiwa

Nana na k'ok'arin kisan kai.

Hakan yasa ya yanke mata hukuncin kisa kai tsaye sbd tayu yunk'urin kisa ba sau 1 ba, tunda hujjoji sun nuna cewar tun yaron yana ciki taso ta kashesa.

Hakan ba k'aramin bugun xuciya ya jawa Nana ba, alokacin ta sume cikin kanta.

Kotun ya d'au surutu, Alk'ali ya buga order sannan akai shiru.

Yan sanda ne suka d'agata aka.fita da ita, alk'ali yace xa'a sanya ranar yimata rataya idan ta farfad'o.

Kowa ya watse xuwa gidansa, mutane se xagin Nana sukeyi sbd yadda sukaji labarin amintakar dake tsakaninta da jawahir tun yarinta.

Nana kuwa da aka kaita asibiti, likitoci sukayi iya gwahe gwajensu kafun a farfad'o hkn ya tabbatar musu cewar zuciyarta ya buga sannan tasamu paralysed.

Yan sanda se da suka tausaya mata amma ita ta jawowa kanta.

Kwananta uku a asibiti batasan inda take ba sannan ta dawo hayyacinta.

Numfashinta sama sama take cewa "ku kiramin Jawahir dan Allah."

Wata yar sanda tace "a gaban namu xaki kashe ta ko meye?"

Tace "ku temakeni kada na mutu ban nemi gafarar ta ba, tunda nake duniya bbu wanda na cutar irin cutarwar da nayiwa.jawahir ku temakeni."

Cikin kuka ta k'arisa maganar nata.

Shugabansu sukayi wa waya, suka sanar masa, yace  ba jimawa xai xo.

Shikuma dr ya kira ya sanarwa abunda ke faruwa, dr yace "ina tsoron ta cutarmin mata fa?"

Police din yace "ba komai dr muma xamuxo bata isa tayi mata komai ba tunda muna.nan, kuma tasamu paralysed.kaga tashi ma se in an d'agata."

dr yace "toh bakomai xamu taho tare insha'Allah."

Ya kalli jawahir dake kusa dashi yace "Nana tanason ganinki, wai xata nemi yafiyarki."

Wasu hawaye suka biyo fuskar ta tace "nariga na yafewa nana tun ba yau ba nikam."

.yace "mu je dai in bbu matsala koh?"

Ta mik'e tasa hijab, be tsaida motonsa ba se a asibiti.

Ta bi Nana da kallo itama Nanan kallonta takeyi tace "jawahir ki yafemin dan allah..kimin."

Jawahir tayi saurin cewa "na yafe miki Nana kibar rok'ona, tun ba yau ba na yafe miki."

Hawaye ne a idanunta sosai tace "Nagode Jawahir, tabbas kin nunamin halaccin aminci, nikuma na nuna miki illar aminci (by Sadnaf) amma nayi nadamar ayyukana a yanxu, na tabbata xan shiga cikin kundin tarihin duniya a matsayin wacce ta toxarta kawance da aminci, a dalili na mutane da yawa xasu daina yadda da junansu, jawahir ki temakeni ki rokamun mus'ab da shahid da Aaseey su yafe min abunda nai musu, kuma ki fad'amin cewar har yanxun kina sona please"

Jawahir ta rushe da kuka sannan tace "ba komai Nana suma xasu yafe miki insha'Allah, sannan kuma i still love yhu tunda kin yi nadamar ayyukan ki."

Nana ta mik'o hanunta wa Jawahir tace "ki rik'e hanuna jawahir inji dumin jikin ki da na jima banji ba."

Jawahir xuciyarta 1 ta mik'awa Nana hanunta tana cewa "Nana kibar kuka ina miki fatan alh...."

Kafun jawahir ta k'arisa Nana tayi wani irin numfashi, lokaci 1 ta janye fuskarta daga kallonsu, dukansu hankalinsu yayi kanta.

Dr ya koma gefen da fuskarta yake ya sanya hannunsa kusada hancinta.

Ba jimawa ya d'ago kansa tareda rufeta da zanin dake kan gadon.

Jawahir a kid'ime tace "dr meye?"

Yace "se hkr, Nana is gone, ta yi tfy na har abada."

Jawahir wani jiri ne ya d'ebe ta dr ya tallafo ta ya fice da ita se motonsa.

Kai tsaye gidansu ya nufa, part insu ya kaita ya kwantar kan kujera

Yasamo ruwa ya yayyafa mata ruwa, nan take ta farfad'o tana ambaton sunan Nana.

A hankali ya.rungume ta yana lallashinta da cewa "kiyi hkr matar likita, nasan yadda kikeji aranki sbd rashin mutum ba k'aramin rashi bane, amma kiyi hkr kiyi mata fatan samun gafara a wajen ubangijinta, wanna shine abunda tafi buk'ata a yanxu."

Wasu zafafan hawaye suka biyo.idanu Jawahir, ayyah she missed her wicjed frnd. Tai ajiyar xuciya tareda cewa "Allah ka jik'an Nana, ka amsheta a matsayin baiwarka me tsarki wacce tati nadama tareda tuba akan laifukanta."

Ta maida kanta jikin dr tana tinano rayuwar da sukayi tareda Nana a baya tun lokacin da Suke k'awance, Allah sarki rayuwa, yau mune gobe ba mu bane, shuka khairi se ka girbi khairi.

Aaseey, Jawahir da sajida duk sunje sunyi wa mum d'in Nana ta'aziyya, itama seda ta rok'i gafarar Jawahir tukunna

Ranar suna aka yi shagali tareda sanyawa yaron Aaseey suna Abbas sunan babanta kenan, amma ana kiransa shuraim.

*3 years later.*
Jawahir ta sungumo yaranta twins mace da namiji, akasha shagalin suna aka sanyawa namijin suna mus'ab macen kuma Aaseeya.

Shahid ya xama babban yaro har ya shiga nursery skul, da gudu ya shigo yayi wurgi da jakarsa gefe yana cewa "mummy ina twins d'ina?"

Tace "twins d'inka suna bacci a d'aki."

Yace "toh mummy ki tashesu muje gidan umma Aaseey muyi wasa da twins d'inta da Yaya shuraim."

Tace "Toh my little doctor, ka bari in kaci abinchi ka huta se muje."

"Toh mummy, daddy yaje hospital yau?"

"Eh yana can hospital, d'ayan daddy'n ka ma yace gobe yanaso kaje kayi masa kwana biyu."

Yace "mummy friends d'ina one daddy suke dashi nikuma i have two,  se sukace wai ni dangata ne, mummy wat does d'angata means?"
.
Tai murmushi tace "d'an gata means wanda ake ji dashi ake sonsa da yawa."

"Yeeh mummy, dat means kina sona dayawa haka both daddies d'ina ma, da aunty sajida itama

tana sona da yawa duk baxaku dakeni ba koh,"

Jawahir tace "in bakayi laifi ba bbu me duka mana kai insha'Allah."

"Toh mummy, let me change my skul uniform se inxo in fada miki mafarkin da nayi yau."

"Mafarki kuma my little doctor?"

"Yes mummy jiya nayi mafarkin mami ta goyeni.".

Ya haura steps din ya canxa kaya sannan ya dawo ta kama hanunsa suka wuce dining.

Ta xuba musu abinci suka fara ci, doctor shahid yai sallama, dukansu suka amsa masa ya k'ariso ya rungume shahid tabaya yana cewa "my son ya skul? An dawo Ify?"
. yace "Ify lau daddy, aunty ta koya mana illnes da causes of illness."
Dr shahid yace "yayi kyau, ina fatan ka fahimchi komai,"

"Yes daddy."

Dr shahid yace "ok wat if islamiyya skul?"

"Jiya anyi mana suratul kafirun."

"Yauwa my son. Allah ya k'ara ilimi da albarka."

Ya sake shahid ya kalli jawahir dake kallonsu gwanin sha'awa.

Yace "matar likita kin share likita koh?"

Tai smiling tCe "na ga likita yana busy da yaronsa ne shiyasa."

Ya karb'i spoon d'in hanunta ya ajiye ya mik'ar da ita tsaye yace "bbu welcome back yau kuma?"

Tai murmushi tayi pointing shahid da hanunta. Yace "ok" ya jata parlour tareda rufe idanunsa.

Ta manna masa wani hot kiss sannan tace "welcom back my doctor, ya ayyuka? Ya sister Sajida?"

.yai murmushi tareda cewa "tnx yhu, aiki alhmdlh, sis sajida kuma tashiga month in haihuwa yau mus'ab ya xo ya karb'a mata hutu."

Tai tsalle tace "woow mun kusa shan bidiri ashe."

Yace "hmm, daga ansha bidiri agidan sajida da mus'ab se gidan yaya sahib da meenal."

Tace "Da gaske yaya? Meenal ma tanada ciki?"

Yace "yes ofcourse, yau sunje asibitin mu, ciii har 3months ma kuwa.".

Tace "oh Allah alhmdllh, mun gode maka godiya me yawa."

Yace "daga gidan yaya sahib kuma se gidan likita da matarsa."

Tace "haba dai, kwata kwata fa twins watansu baikai tara ba, nikam ba yanxu ba, ta nok'e kafad'a."

Yai dariya yace "inaso ki taramin yarane fa da yawa yar mufi Aaseey."

Tace "toh ai Aaseey'n da d'aya tafimu, daga twins inta se shuraim se Ahmad kuma itama Ahmad d'inta watansa biyar ne kacal, kaga mun kusa mu isota ai."

Yai dariya yace "shikenan, kallon me kikemin d'axu nida shahid d'ina?"

Tace "kawai ina ganin yadda kakeson yaron ne, ko twins baka damu dasu ba kamar yadda ka damu da shahid, shine abun naku yake burgeni".

Yace "toh in banda abunki waye nafara gani acikinsu? Aidole shi xan fiso infi sabawa dashi, ko kin yadda in nayi sabuwar amarya in manta dake infi sonta?"

Nan da nan fuskarta ya canxa tace "savuwar amarya kuma likita?"
Yai murmushi ya d'aga mata gira sannan yace "yes very soon xata xo ai."

Bata jira amsar sa ba ta wuce bedroom.da gudu, ta hau gado tana maida numfashi, lokaci 1xufa ya keto mata taji kanta yad'au chaji, wasu xagafan hawaye ke fita a idanunta wanda batasanda xuwansu ba, batasan.wani.irin so take.yiwa dr shahid ba bata san yaushe tafara kishin sa ba har haka.

Da sauri ya biyota shima kan gadon yahau tareda talafo fuskarta yanda yaga hawaye a idanunta shine abunda ya d'aga masa hnkl, yace "Babylove meya samin ke kuka? Maganar da na fad'a neh?"

Ta gyad'a kai yace "haba dai Matar likita, ai kinsan ke 1 ce a raina daga ke bbu wata, ko baki sani bane kina shiga xuciyata kika sa key? Toh haka kika yiwa gida nan ma, kina shiga kikasa lock bbu me shigowa a matsayin matar likita ke 1 ce matar likita, kamr yadda likita yake naki ke 1 har abada."

Wani sanyine ya xiyarci xuciyar ta batasan sanda tai murmushi ba tace "really?"

Yace "yes really matar likita, likita nakine ke d'aya duk wadda ta so shi ma se na tayaki cin k'walarta."

Ta tuntsure da dariya tace "Toh Allah yasa haka har abada".
Yace "amee, muje ki k'arisa cin abincinki"

Tace "ai da na ganka naji na k'oshi da yunwar."

Yace "u'um pa?"
Tace "dagaske," yace " toh muje ki tayani inci nawa."

Suka mik'e yana rik'e da ita, ya kaita har dining sannan suka samu shahid yana rik'e da wasu hotuna,
ya kallesu yace "daddy wayene a hoton nan?"

Dukansu suka kai idanunsu kan hoton, jawahir ta kauda kai gefe dr shahid yace "she's mummy's friend Nana sunanta."

Yace "toh ai bata xuwa gun mummy ban tab'a ganinta ba."

Dr yace "she's late, ta rasu tun kana one year old."

"Allah sarki mummy na tayi kuka koh?"

yace " tayi mana, kai yanxu idan abokin ka ya rasu ai xakayi kuka toh itama hkne."

Yace "mummy itama kafun ta rasu tana sonki irin umma Aaseey koh? Naga akwai.hoton ta da yawa a cikin hotunan d'akina."

Ta juyo ta share hawayen idanunta ta rungume shahid tace "tana sona sosai, kuma ta koyamin darasi da yawa a rayuwa, sannan kafun tabar duniya tabani sak'o in baka, cewar ka yafe mata akwai laifin da tayi maka, ka yafe mata koh my son?"

Yace "ni kuma? Mummy ba kince tana sonki ba toh meyasa tamin laifi?"

Tace "tayi a kuskure ne shiyasa tace mu yafe mata, nikuma na yafe tun tana nan kaima ka yafe mata tunda k'awa tace ina sonta da yawa kamar umma Aaseey."

Yace "mummy na yafe mata tunda tana sonki, kuma xanyi mata addu'a in nayi sallah yanda malam yace muyiwa wanda ya rasu."

Tace "yauwa, dats my son. I love yhu so so much".

Ta rungumesa ajikinta.

Dr ya d'auko plate in powder da foundation inta ya goge mata hawaye sannan ya gyara mata fuska.

Ta kallesa tace "se kace artist? Kada kaxama na mata na mata fa."

Yace "Akanki xanyi komai my wife."

Tayi murmushi ta rungume mijinta, rr shahid ya jawo shahid ma jikinsu ya bud'e camerar wayarsa xai musu selfie.

Dukansu sukayi murmushi harda hakwaransu a waje sannan dr ya d'auka.
_*KASHAF*_📱

Nima da sauri naje dan insamu shiga amma ina anriga anyi bandani.

_*Tammat bi hamdillah*_
_*Se mun had'u a sanon novel ina dalilin so, wanda xan fara postin d'insa 1st june insha'Allah.*_

_*Special tnx to Muhammad Umar Bhali's Family, Allah yabar kauna, ya k'ara had'a kanmu cikin alkairi.*_

_*Bunch of tnx specially To jamila. Maman khausar godiya dubu da saka chaji.*_

_*Baxan manta daku ba k'awayen arxik'i.*_

Rabi'atu kunun xakin xuciya.
Rukeey Ammar.
Aunty Asma'u.
Habiba kakar kowa.
Maryam prosecutor.
Rabi'atu health
Amina meenaye.
Maryam amarya.
Ummulkhulsum
My Aaseey white.
Nana khadijat.

Barrister.
Naseeba Nancy.
Aysha fullo.

_*My best online writers.*_
_*Miemiebie.*_
_*Dija waziri.*_
_*Asykhaleel.*_
_*Hauwa jidda Aliyyu.*_

_*my best online friends*_
_*jidda magarya*_
_*Shukry yola.*_
_*Khadija sokoto.*_

_*D whole buk is dedicated to AYSHA AUWAL LIJI (KHAUSAR) I LOVE YHU ENERMOUSLY SWEET DOTA, Allah barni dake.*_

_*Kharyma (Sajna ) ce!*_